# Takaitaccen Tarihin Annabi (s a w)

## Tare da

## Fa'idodin kowane Darasi

Dan masu Magana da harshen Hausa

## Wallafar

## Abu zakariyya Arrigasi

## All rights reserved

E-MAIL: Abuzakariyya.uk@gmail.com

# مُقَدَّمَةُ الْمُؤَلِّفِ

## بِسْمِ اللهِ الرَّحْمَنِ الرَّحِيمِ

الْحَمْدُ لِلَّهِ الَّذِي خَصَّ نَبِيَّنَا مُحَمَّدًا ﷺ بِالْخَصَائِصِ الْجَلِيلَةِ، وَفَضَّلَهُ عَلَى غَيْرِهِ مِنَ الْمَخْلُوقَاتِ، وَجَعَلَ أُمَّتَهُ خَيْرَ أُمَّةٍ أُخْرِجَتْ لِلنَّاسِ تَأْمُرُونَ بِالْمَعْرُوفِ وَتَنْهَوْنَ عَنِ الْمُنْكَرِ، وَنَسَخَ بِدِينِهِ سَائِرَ الْأَدْيَانِ السَّمَاوِيَّةِ الْمَاضِيَةِ، فَتَبَارَكَ اللهُ الْمَوْلَى جَلَّ وَعَلَا. وَصَلَاةً وَسَلَامًا عَلَى هَذَا النَّبِيِّ حَامِلِ لِوَاءِ الْحَمْدِ وَصَاحِبِ مَقَامِ الْمَحْمُودِ الْأَمِينِ، وَعَلَى آلِهِ وَصَحْبِهِ الْجِيلِ الْفَرِيدِ الَّذِي لَمْ تَتَشَرَّفِ الْبَشَرِيَّةُ عَلَى مِثْلِهِ عَبْرَ تَارِيخِهَا الطَّوِيلِ، وَمَنْ سَارَ عَلَى دَرْبِهِمْ بِإِحْسَانٍ إِلَى يَوْمِ الْمَعَادِ.

أَمَّا بَعْدُ: فَإِنَّ لِمَعْرِفَةِ السِّيرَةِ النَّبَوِيَّةِ أَهْمِيَّةٌ بَالِغَةٌ فِي حَيَاةِ الْمُسْلِمِ، لِمَا تَضَمَّنَتْهُ مِنْ مَكَارِمِ الْأَخْلَاقِ الْحَمِيدَةِ، وَلَا شَكَّ أَنَّ سِيرَةَ نَبِيِّنَا ﷺ مَمْلُوءَةٌ بِذَلِكَ، وَالْغَرَضُ فِي مَعْرِفَةِ سِيرَتِهِ ﷺ الْعَطِرَةِ الْاقْتِدَاءُ بِهِ وَالسَّيْرُ عَلَى دَرْبِهِ وَمِنْوَالِهِ لَا لِمُجَرَّدِ التَّأْنِيسِ وَالْاسْتِنْشَاطِ، لِأَنَّ سِيرَتَهُ ﷺ عِبَارَةٌ عَنْ أَخْلَاقٍ حَمِيدَةٍ مَرْمُوقَةٍ اتَّصَفَتْ بِهَا هَذِهِ الشَّخْصِيَّةُ النَّبَوِيَّةُ، وَلِمَا رَأَيْتُ مِنْ قِلَّةِ كُتُبِ السِّيرَةِ الَّتِي سُطِرَتْ بِاللُّغَةِ الْهَوْسِيَّةِ، وَفْقَ الْمَنْهَجِ الْعِلْمِي، حَمَلَنِي ذَلِكَ عَلَى الْقِيَامِ بِالتَّسْطِيرِ عَلَى هَذِهِ الصَّفَحَاتِ الْبَيْضَاءِ الَّتِي تُدَنْدِنُ حَوْلَ حَيَاتِهِ ﷺ بِهَذِهِ اللُّغَةِ الَّتِي يَنْطِقُ بِهَا مَا يَزِيدُ عَلَى مِائَةِ مِلْيُونِ شَخْصٍ فِي الْمَنْطِقَةِ الْإِفْرِيقِيَّةِ، لَاسِيَمَا الْإِفْرِيقِيَّةِ الْغَرْبِيَّةِ، خُصُوصًا جُمْهُورِيَّتِنَا نَيْجِيرِيَا الَّتِي هِيَ أَكْبَرُ تَجَمُّعٍ لِلنَّاطِقِينَ بِهَذِهِ اللُّغَةِ الْمُبَارَكَةِ، وَهِيَ أَكْبَرُ دَوْلَةٍ هَوْسِيَّةٍ فِي الْعَالَمِ

مِنْ جِهَةِ التَّعْدَادِ السُّكَّانِي، وَلِذَا عَزَمْتُ عَلَى جَمْعِ شَيْءٍ يَسِيرٍ مِنْ سِيرَتِهِ ﷺ بِهَذِهِ اللُّغَةِ، لِأَنَّ هُنَاكَ أُنَاسًا كَثِيرِينَ لَا يَسْتَطِيعُونَ قِرَاءَةَ كُتُبِ سِيرَتِهِ ﷺ الْمُدَوَّنَةِ بِالْعَرَبِيَّةِ. ثُمَّ إِنَّنِي لَا أُطْنِبُ فِي ذَلِكَ حَتَّى يَكُونَ الْكِتَابُ كَبِيرَ الْحَجْمِ، بَلْ أَخْتَصِرُهُ اخْتِصَارًا مُتَوَسَّطًا غَيْرَ مُخِلٍ بِالْمَعْنَى، فَنَسْأَلُ اللهَ تَبَارَكَ وَتَعَالَى أَنْ يَتَقَبَّلَ مِنَّا عَمَلَنَا هَذَا وَيَكْتُبَ لَهُ الْقَبُولَ، وَأَنْ يَنْفَعَ بِهِ الْإِسْلَامَ وَالْمُسْلِمِينَ، وَهُوَ مِنْ وَرَاءِ الْقَصْدِ وَيَهْدِي السَّبِيلَ.

**أَخُوكُمْ فِي اللهِ**

**أَبُو زَكَرِيَّا الرِّغَاسِيُّ**

حُرِّرَ فِي يَوْمِ الْخَمِيسِ ضُحًى 26 – 8 – 1442هـ الْمُوَافِقُ 8 – 4 – 2021م

# Gabatarwa

Dukkan yabo da godiya da kirari da jinjina sun tabbata ga Allah maɗaukakin sarki wanda yai mana bai'wa da kasancewa cikin al,ummar Annabi Muhammad (saw) farin jakada mafi daraja da ɗaukaka daga cikin Annabawa da ma dukkan halittu gaba ɗaya, tsira da amincin Allah su ƙara tabbata a gareshi da iyalan gidansa tsarkaka da sahabbansa ma'abota annuri da albarka, da duk wanda ya bi tafarkinsu da kyautatawa har izuwa ranar tsayuwa gaban Allah dan hisabi.

Bayan haka: haƙiƙa sanin tarihin Annabi (saw) ya na da matukar mahimmanci a rayuwar musulmi saboda abunda ya ƙunsa na daga ƙyawawan ɗabi'u da mu'amaloli, domin manufar karanta tarihin annabi (saw) shi ne dan ayi koyi da abunda ya ƙunsa na daga kyawawan ɗabi'u ba dan a yi nishadi ba kawai, duba da hakane naga ya dace ace an samar da wani littafi wanda zai yi bayani akan rayuwar Annabi (saw) da harshen hausa bisa doran ilimi da dogaro da ingantattun littattafan da a ka rubuta a wannan fannin waɗanda suka samu kyakkyawan ƙabuli wurin al'umma, kamar littafin: (siratun – nabawiyya) na Abdulmalik bini hisham Annahawi, wanda talkisi ne na (sirar) muhammad ibini Ishaƙ Almuɗɗalibi, da kuma (sira) ta ibini Kassir, da sauran shahararrun littattafan sira waɗanda aka rubuta a zamunan da suka shuɗe da ma na wannan zamani, saboda masu magana da wannan harshen waɗanda sune mafi yawa a nahiyar Afuruka ta yamma, musamman ƙasa Naijiriya wacce ta fi kowace ƙasa yawan masu magana da wannan harshen mai albarka, saboda hakane na tanadi wannan littafin dan suma su

anfana da abunda tarihin farin jakada ya ƙunsa na ɗabi,u managarta, saboda ba kowa ba ne ya iya larabci, muna fatan Allah ya sanya wannan aikin acikin kyawawan ayyukan mu, ya kuma anfanar da waɗanda aka yi donsu.

**Ɗan'uwan ku a musulunci**

**Abu zakariyya Arrigasi**

Ranar Alhamis da hantsi: 26 – 8 – 1442,h. Dai-dai da: 8 – 4 – 2021, m.

# Larabawa gabanin Musulunci

Ya na da mahimmanci mu san suwaye Larabawa gabanin zuwan musulunci don abun zai fi fitowa fili, saboda su ne mutanan da Annabi (saw) ya taso a cikinsu kuma aka aiko shi cikinsu.

Da farko dai su Larabawa sun kasance suna zaune a yankin da ya ke da yawan sahara da tsandauri wanda ya fi shahara da (jaziratul Arab) wacce ta yi iyaka da baharul Ahamaru ta yammaci, da wani bangare na garuruwan Iraƙi ta gabashi, da baharul Arab ta kudanci, da kuma garuruwan siriya ta arewaci.

Larabawa kashi uku ne ta fuskar tsatson da suka fito, gasu nan kamar haka:

1- Al'arbul ba'idatu: su ne larabawan da suka shuɗe shekaru aru-aru waɗanda a yanzu sun ƙare gaba ɗaya, kamar su Adawa da samudawa da Amaliƙawa da makamantan su.
2- Al'arbul aribatu: sune larabawan da suka fito ta tsatson Yashjabu ɗan ya,arabu ɗan ƙahɗan, cibiyar su ita ce yamen.
3- Al'arbul musta'ariba: sune larabawan da suka fito ta tsatson Annabi Isma'ila ɗan Annabi Ibrahim (as) ana kiran su da Al'arbul Adananiyyatu.
Ana cewa annabi Isma,ila shi ne wanda ya fara magana da harshen larabci kamar yadda Ya'aƙubi ya hakaito acikin tarihinsa, sai dai tarihi ba ya goyan bayan wannan maganar.

## ADDINAN LARABAWA KAFUN MUSULUNCI

Mafi yawancin larabawa suna bin addinin Annabi Ibrahim ne (as) a farkon al'amari ba yan zamani ya tsawaita garesu sai aka samu wani

mutum mai suna Amru ɗan Luhayyi shugaban ƙabilar kuza,a wanda ya shahara DA kyawawan lamura da kuma nuna kulawa ga lamuran addini, wanda hakan ya sa mutane suka ƙaunace shi suke masa kallon wani babban waliyyi, ananan a haka wata rana ya yi balaguro zuwa ƙasar siriya ya ga yadda suke bautar gumaka sai hakan ya ba shi sha'awa ya yi tsanmanin wani abin arzikine, sai ya dawo da wani gunki wanda ake kira (Hubal) ya sanya shi acikin Ka'aba, ya kwaɗaitar da mutanen Makka akan bauta masa, tun daga wannan lokacin bautar gumaka ta watsu acikin larabawan makka da maƙotansu, wannan shi ne asalin bautar gumaka acikin Larabawa.

## DANGANTAKAR ANNABI (SAW)

nasabar Annabi (saw) mai tsarki ita ce kamar haka: Muhammad ɗan Abdullahi ɗan Abdulmuɗɗalib ɗan Hashim ɗan Abdumanaf ɗan ƙusaiyyi ɗan Kilab ɗan Murra ɗan Ka'abu ɗan Lu'ayyu ɗan Galibu ɗan Fihar ɗan Malik ɗan Nadar ɗan Kinana ɗan Kuzai'ma ɗan Mudrika ɗan Iliyasu ɗan Mudar ɗan Nizar ɗan Mu'addin ɗan Adnan.

Wannan shi ne abin da malamai masana nasaba suka yi ittifaƙi akan shi dan gane da nasabar annabtaka mai tsarki, wato zuwa Adnan, amma Abin da ya gota Adnan to akwai saɓani mai girma game da adadin sunayen kamar yadda Abul Hasan ibnul Asir ya bayyana a cikin (Asadul gaba)  da kuma ibni Abdulbarri a cikin (Al'isti'ab) wanda da shi ibnul Asir ya dogara game da hakan, imamul Bagawi ba yan ya koro nasaba zuwa Adnan a cikin (sharhus sunna) ya ke cewa duk abin da aka anbata na daga nasaba ɗoriya akan Adnan ba ya inganta.

Shi Abdulmuɗɗalib sunansa (Shai'ba) kamar yadda ibnu Is'haƙ ya faɗa ibnu Hisham ya inganta shi acikin Sirah, shi kuma Hashim sunansa (Amru) shi kuma Abdumanaf sunansa (Almugira) shi kuma ƙusayyu sunansa (Zai'du) shi kuma Fihar shi ne wanda ake wa laƙabi da: (Alƙuraish) wanda ake jingina ƙabilar zuwa gare shi, shi kuma Nadar shi ne (ƙai'su) shi kuma Mudrika sunansa (Amir)

Haƙiƙa nasabar Annabi (saw) nasaba ce mafi daraja mafi tsarki mafi ɗaukaka wacce ba ta da tamka.

## Auren Abdullahi da Aminatu

Abdullahi shi ne mahaifin Annabi (saw) mahaifiyarsa kuma ita ce Aminatu 'Yar Wahabu ɗan Abdumanaf ɗan Zuhratu ɗan Kilab, wato Aminatu ta yi tarayya da Abdullahi ta wajen kakansa na biyar.

Yayin da Abdullahi ya kai munzali sai mahaifinsa Abdulmuɗɗalib ya nema masa auren Aminatu a wajen babanta Wahabu ɗan Abdu-manaf wanda shine mafi ɗaukaka kuma jagora acikin ƙabilar banu Zuhra, sai ya aurar masa da ita, a wannan lokacin Aminatu ta kasance mafi daraja da ɗaukaka a cikin ƙabilar ƙuraish domin ba-banta Wahabu shine shugaban ƙabilar zuhra kuma mafi daraja da nasaba acikin ƙabilar, Abdullahi ya tare da ita a garin makka, ba yan wani lokaci ƙalilan sai ya yi tafiya zuwa Sham yayin da ya ke kan hanyarsa ta dawowa a cikin tawagar ƙuraish sai ya yada zango a Madina saboda rashin lafiya sai rai ya yi halinsa anan, aka binne shi a gidan wani bawan Allah mai suna (Nabigatujju'udi) a lokacin da ya rasu ya na da shekara ashirin da biyar (25) hakan ya faru kafun haihuwar Annabi (saw) kamar yadda ɗaukacin malaman tarihi suka tafi akan hakan, bai bar wani abu mai yawa ba na daga dukiya face

raƙuma biyar (5) da 'Yan tumaki da awaki, sai kuma kuyanga guda ɗaya mai suna (Ummu Ai'man Barakatul Habashiyya) wacce ta na ɗaya daga cikin matan da suka reni Annabi (saw).

## Hai'huwar Annabi (saw)

An haifi Annabi (saw) a unguwar banu Hashim dake Makka a safiyar ranar litinin sha biyu ga watan rabi'ul auwal (12) a bisa zance mafi shahara, hakan ya farune a shekarar Giwa, wanda hakan yai dai-dai da ashirin da biyu ga watan afrilu shekara ta ɗari biyar da saba'in da ɗaya (571) miladiyya.

Dalilin anbaton shekarar haihuwarsa da shekarar giwa kuwa shine sarkin Habasha na wancan lokacin mai suna (Abarahata) ya gina wata babbar coci a garin Sana'a dake yamen, domin ya juyo da hankulan larabawa zuwa gareta ya raba su da Ka'aba, sai wani daga cikin banu kinana ya ji labarin haka, sai ya yi kashi ya yayyaɓa wa wannan cocin, yayin da labari ya je kunnen Abarahata sai ya yi fushi ya rantse cewa sai ya rusa ka,aba, ya shirya gagarumar runduna zuwa Makka a cikinta akwai wata ƙatuwar giwa mai suna Mahmud, daga ƙarshe dai Allah ya halakar da wannan rundunar ta hanyar aiko musu da tsuntsaye ɗauke da bama-baman wuta kamar yadda ya ba da labari a cikin Suratul fili.

## Alamomin hai'huwar Annabi (saw)

Haƙiƙa manyan alamomi sun bayyana waɗanda suke ishara zuwa ga cewa Duniya zata karɓi baƙoncin wani babban mutun mai girman lamari, haƙiƙa mahaifiyarsa ta ba da labarin cewa lokacin da ta haife shi ta ga wani haske ya fito daga gaban ta wanda ya

haskaka fadar sarautar Sham kamar yadda ibnu Sa'ad ya ruwaito a cikin (Aɗɗabaƙat) sannan kuma ta ba da labarin cewa lokacin da ta haife shi ba ta ji abin da mata suke ji ba na ciwon naƙuda, sannan an ruwaito cewa lokacin da aka haife shi sai da ɗakuna goma sha huɗu na fadar sarautar kisra suka faɗi sannan wutar da majusawa suke bautamawa shekaru aru-aru ta mutu cocinan da suke gefen (Buhai'ratu sawa) suka ruguje kamar yadda imamul Bai'haƙi ya ruwaito acikin (Dala'ilun Nubuwati) da Ɗabari acikin tarihinsa.

An ruwaito cewa an haife shi da kaciyarsa, Al'hafiz ibnul ƙayyim ya ce babu wani hadisi ingantacce akan haka kamar yadda ya faɗa acikin (Al – Hadayun Nabawi) kuma koda ma hakan ya inganta ba wani abin azo a gani bane jingina hakan ga Annabi (saw) domin ana samun jariran da ake haihuwarsu da kaciyarsu, shi kuma Annabi (saw) abin al'ajabinsa ya fi gaban haka.

Lokacin da Amina ta haifi Annabi (saw) sai ta aika a faɗa ma kakansa Abdulmuɗɗalib, sai ya zo ya na farin ciki ya ɗauke shi ya shigar da shi cikin Ka'aba yai godiya ga Allah kana ya yi masa addu'a ya sa masa suna Muhammad, wanda larabawa basu san wannan sunan ba gabanin haka.

## Shayar da Annabi (saw)

Wacce ta fara shayar da Annabi (saw) ita ce mahaifiyar sa Aminatu Ƴar Wahabu sannan sai Suwai'batul Aslamiyya Ƴantacciyar baiwar Abu Lahab a lokacin ta na shayar da ɗanta mai suna masruh, gabanin haka ta shayar da Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib baffan Annabi (saw) sannan bayan ta sai Halima Ƴar Abu Zu'aib Assa'adiya matar Haris bini Abdul'uzza wanda ake wa alkunya da Abu Kabasha,

haƙiƙa Halimatussa'adiyya ta ga albarka da abin al'ajabi alokacin da ta ke shayar da Annabi (saw) na daga yalwar arziki da kuzarin raƙuminta da makamancin haka, ita ce wacce Annabi (saw) ya fi daɗewa awurinta.

Watarana Annabi (saw) ya na cikin yara ya na wasa a lokacin ya na ɗan shekara huɗu a Duniya, sai Jibrilu (as) ya zo ya riƙe shi ya kwantar da shi ya tsaga kirjinsa ya fito da zuciyarsa ya ciro wata tsoka daga cikinta ya ce wannan shine rabon shaiɗan daga gare ka, sannan sai ya wanke ta acikin wata tasa ta zinariya da ruwan zamzam ya maida ita kamar yadda ta ke, yayin da sauran yaran da ke tare da shi suka ga haka sai suka ruga zuwa wajen mariƙiyarsa wato Halimatussa,adiyya suka gaya mata abin da ke faruwa, sai ta ji tsoro ta mai da shi wurin mahaifiyarsa.

## Rasuwar mahaifiyarsa

Ya na nan wurin mahaifiyarsa har shawon shekara biyu alokacin ya na ɗan shekara shida, sai mahaifiyarsa ta ga dacewar ta kai ziyara zuwa ga ƙabarin mijinta wato mahaifin Annabi (saw) Abdullahi, da ke Madina, sai ta kama hanyar madina tare da marayanta Annabi (saw) da kuma hadimarta Ummu Ai'man da sirikinta Abdulmuɗɗalib, har ta isa ta zauna anan tsawon wata guda kana ta ɗau hanyar dawowa, sai rashin lafiya ya same ta har dai takoma zuwa ga Allah a wani wuri da ake kira da Al'abwa'i da ke tsakanin Makka da Madina.

## Ya dawo ƙarƙashin kulawar kakansa

Daga nan sai kakansa Abdulmuɗɗalib ya dawo da shi Makka ya ci gaba da ba shi kyakkyawar kulawa ta musamman ya fifita shi akan sauran 'Ya'Yansa na ciki, duba da irin halin da ya samu kan shi aciki na rashin bangwaye guda biyu wato babansa da mamarsa, wanda acikin hakan akwai wani ɓoyayyan sirri da hikima ta allantaka, Annabi (saw) bai gushe ba cikin kulawar kakansa har tsawon shekara biyu alokacin ya na ɗan shekara takwas aduniya, a wannan lokacinne Allah ya yi wa kakansa rasuwa.

## Ya dawo ƙarƙashin kulawar baffansa Abu Ɗalib

Daga nan sai ya dawo ƙarƙashin kulawar baffansa Abu Ɗalib, anan ne ya samu gagarumar kulawa da karramawa domin Abu Ɗalib ya yi tsayin daka wajen ganin ya kyautata masa har ta kai ga ya fifitasa akan dukkanin 'Ya'Yansa, ana nan a haka sai wata rana fari ya sami mutanen makka, sai suka nema daga Abu Ɗalib akan ya fito ya yi musu roƙon ruwa, sai ya fito tare da Annabi (saw)  girgije ya na ma Annabi (saw) inuwa duk inda ya yi ya na biye da shi, ba a jimaba sai ga hadari ya haɗu aka kece da ruwa kamar da bakin ƙwarya sai arziki ya yalwata fari ya tafi albarkacin Annabi (saw) wannan ƙissa Hai'sami ya kawo ta acikin (majma'uzzawa'id)

## ƙissar Annabi (saw) da Bahira (Arrahib)

Yayin da Annabi (saw) ya kai shekara goma sha biyu a rayuwarsa sai Abu Ɗalib ya yi balaguro zuwa sham (siriya) tare da shi har suka iso garin Basra, to awannan garin akwai wani mai yawan ibada aƙarƙashin addinin nasara wanda ake kira (Bahira) amma sunansa

(Jarjis) su na sauka a masaukin su sai wannan mutumin ya fito zuwa garesu ya na bibiyarsu har ya kai ga Annabi (saw) sai ya kama hannunsa ya ce wannan shine shugaban halittu wannan shine manzon Ubangijin halittu, sai Abu Ɗalib da wasu daga cikin dattawan ƙuraishawa suka ce masa ya aka yi kasan haka? Ya ce na gane shine ta hanyar hatimin annabtaka da ke allon kafaɗarsa, sannan kuma akwai anbatonsa acikin littafinmu, da ga nan dai ya roƙi Abu Ɗalib akan ya mai da shi gida kar ya ƙarasa da shi sham saboda gudun maƙiya na da ga yahudawa, sai ya sa aka mai da shi.

## Kiwon tumaki

Annabi (saw) ya ba da labarin cewa babu wani Annabi da aka aiko face ya yi kiwon tumaki, sahabbansa suka tanbaye shi: har kai ya Rasulullah? Ya ce: eh, har ni, na kasance ina ma mutanen Makka kiwon tumakinsu su na bani wasu ʽYan silalla.

Haƙiƙa a cikin kiwon tumaki akwai hikimomi masu tarin yawa, kaɗan da ga cikinsu:

1- Sanya mutun ya goge wajen iya tafiyar da jagorancin mutane, domin duk wanda ya iya tafiyar da lamuran ƙananan Dabbobi to tafiyar da lamuran mutane zai zo masa da sauƙi.
2- Koyon haƙuri da juriya, saboda sha,anin Dabbobi sai haƙuri, ka taro wancan wancan ya kuma ɓallewa.
3- Tausayi da jinƙai, domin tsayin Dakar sa wajen ganin ya kiyayesu da ga miyagun Dabbobi masu farautarsu da kuma ɓarayi da kula da su wajen shayarwa, dukkan wannan ya na haifar da tausayi, domin duk wanda ya ji tausayin dabbobi tabbas zai ji tausayin mutane.

4- ishara zuwa ga cewa addinin musulunci ba ya goyan bayan zaman kashe wando, a,a kowa ya tashi ya nema na kansa.

## Auren Annabi (saw) da sayyada Kadija (ra)

Yayin da Annabi (saw) ya kai shekara ashirin da biyar a rayuwarsa sai ya yi balaguro zuwa siriya dan yin kasuwanci a cikin dukiyar Kadija (ra) wacce ta kasance babbar attajira ta na da yara da yawa masu juya mata dukiya ta hanyar fatauci zuwa gari gari ta na biyansu, yayin da labarin Annabi (saw) ya risketa na daga gaskiyarsa da amanarsa da kyawawan halayensa maɗaukaka sai ta buƙaci da ya kasance ɗaya daga cikin masu juya mata dukiyarta za ta ruɓanya masa abin da ta ke ba sauran yaran ta na daga lada kamar yadda ibnu Sa'ad ya ruwaito acikin (Aḍḍabaƙat) sai Annabi (saw) ya yarda ya fita ya yi fatauci tare da yaronta Mai'sara, aka samu gagarumar riba wacce ba,a taɓa samun kwatankwacinta ba, yayin da kadija ta ga haka kuma ta ƙara samun labarin karamcinsa da kyawawan halayensa a wurin yaronta Mai'sara, sai ta bijiro masa da maganar aure, wanda gabanin haka manyan mutane masu mulki da kuɗi sun neme ta da aure amma taƙi saurarsu, daga ƙarshe dai aka ɗaura musu aure bayan manya sun shiga cikin lamarin, wanda Annaba (saw) ya aure ta ya na da shekara ashirin da biyar ita kuma ta na da ashirin da takwas, wannan shine zance mafi inganci a wurin ƙwararrun malaman tarihi, Kadija ita ce matarsa ta farko bai taɓa ma ta kishiya ba har ta koma zuwa ga Allah, sannan ita ce ta haifa masa dukkan ƳaƳansa ban da Ibrahim domin shi mariyatul ƙibɗiya ce ta haife shi, haƙiƙa Kadija ta bada gagarumar gudummuwa a tafiyar da'awa ta Annabi (saw) alkairin Allah ya kai mata.

## Tarayyar Annabi (saw) da ƙurai'shawa wajen gina Ka'aba

A yayin da Annabi (saw) ya kai shekara talatin da biyar a rayuwarsa a wannan lokacin ne ƙurai'shawa suka tsayu wajen sake jaddada ginin Ka,aba, wanda daman can tsawonta bai wuce zira'i tara ba tun dai yadda take azamanin annabi Isma'il (as) sannan kuma katangunta sun fara samun matsala, a yayin kuma da aka samu ɓarayi suka sace taskarta da ke cikinta wacce da ita ake anfani wajen kula da Ka'aba, Annabi (saw) ya yi musharaka da ƙuraishawa wurin wannan aikin na gayya, kuma ya nuna bajinta ƙwarai da gaske, amanarsa da gaskiyarsa da hikimarsa da fasaharsa sun kuma bayyana ga ƙurai'shawa, wannan ya farune kafun annabta da shekara biyar.

## Annabci

A yayin da Annabi (saw) yake gab da cika shekaru arba'in arayuwarsa, sai aka sanya masa san keɓancewa a wuri mai natsuwa marar hayaniya, ya kasance ya na zuwa kogon Hira'i da ke dutsen Jabalun-nur, wanda tsakanin shi da Madina tafiyar kilomita biyu ne, kogon ya kasance ya na da faɗin zira'i ɗaya da kwatan zira'i, tsawo kuma zira'i huɗu da zira'in ƙarfe, ya kasance ya na zama a cikinsa tsawon watan ramadana ya na yin tunanin manya manyan halittun Allah masu nuna ƙudurar sa da ƙarfin mulkinsa acikin sa, ya kan yi guzurin abincinsa da abin shansa da ga sayyida Kadija idan sun ƙare sai ya koma ya zo da wasu, duk wannan shirine dan fiskantar manzanci.

A yayin da ya kai shekara arba'in, Allah ya aiko masa da mala'ika Jibrilu (as) wanda shine mala'ikan da allah ya wakilta da isar da

saƙon annabtaka zuwa ga wanda ya zaɓa daga cikin bayinsa, mala’ika Jibrilu ya umarce shi da ya yi karatu, ya ce shi bai taɓa karatu ba, sai Jibrilu (as) ya rike shi ya ɗan matse shi, har sai da aka maimaita hakan sau uku, sai ya biya masa ayoyi guda ukun farko daga suratul Alaƙ ga su kamar haka:

« اقْرَأْ بِسْمِ رَبِّكَ الَّذِي خَلَقَ * خَلَقَ الإِنْسَانَ مِنْ عَلَقٍ * اقْرَأْ وَرَبُّكَ الأَكْرَمُ » العلق: (3 - 1)

Ma,ana: ka yi karatu da sunan ubangijinka wanda ya yi halitta, ya halicci mutun daga gudan jini, ka yi karatu ubangijinka mai karamci ne.

Waɗan nan ayoyi guda uku sune farkon abin da ya fara sauka ga Annabi (saw) na wahayi.

Bayan haka sai Annabi (saw) ya koma gida zuciyarsa na raurawa ya shiga wurin Kadija (ra) ya na cewa ku lulluɓeni ku lulluɓeni, sai nana Kadija ta lulluɓe shi ya samu nutsuwa, sannan ya ba ta labarin duk abin da ya faru da shi, sai ta ce da shi Allah ba zai taɓa tozarta ka ba domin ka na sadar da zumunta ka na ɗaukarwa kan ka abin da ba wajibi ba sannan kana ba wa mabuƙata na da ga abin da Allah ya azurtaka da shi sannan kana shiryawa baƙi liyafa sannan kana taimako akan abubuwan da suke samun mutun na musibu, daga ƙarshe dai ta kai shi wajen wani baffanta mai suna Waraƙatu ɗan Nau’fal, wanda ya na da sani game da addinin nasara har ma ya na rubuta littafin Injila da harshen ibraniyanci, sannan kuma dattijo ne sosai har ma ya makance, a yayin da ta ba shi labarin abin da ya wakana da Annabi (saw) sai ya ce: haƙiƙa wannan shine Manzon da

ya ke zuwa ma Annabi musa (as) ya na nufin mala’ika Jibrilu, ya ce: ina ma dai ina da kuzarin samartaka a yayin da mutanenka za su fitar da kai daga garinka.

**Tanbihi:** mai karatu zai ga muna tsallake wasu abubuwa, muna yin hakane dan taƙaitawa, domin idan ba ka manta ba sunan littafin (Taƙaitaccen tarihin Annabi saw) idan aka ce za a kawo komai da komai to littafin zai yi yawan da mai karatu zai gundura da karantawa, gwara a yi shi tsaka tsaki.

Daga nan sai wahayi ya yanke na ɗan wani lokaci, sannan mala’ika Jibrilu ya kuma sakkowa tare da ayoyi guda biyar na cikin Suratul Mudassir, gasu kamar haka:

« يَا أَيُّهَا الْمُدَثِّرُ * قُمْ فَأَنْذِرْ * وَرَبَّكَ فَكَبِّرْ * وَثِيَابَكَ فَطَهِّرْ * وَالرُّجْزَ فَاهْجُرْ » المدثر: (1 .5)

Ma’ana: ya kai na lulluɓe, tashi ka yi gargaɗi, Ubangijinka kuma ka girmama shi, tufafinka kuma ka tsarkakesu, ƙazanta kuma ka ƙaurace mata (ma’ana: gumaka)

Waɗan nan sune ayoyin da suka fara sauka ta fuskar umarni da isar da risala, su kuma ayoyi ukun da suka gabata na suratul Iƙra’a, sune na farkon sauka ta fuskar tabbatar da annabtaka.

## Farawar Da’awa a sirrance

Annabi (saw) ya fara kira zuwa ga Allah a sirrance bayan saukar ayoyin da suka gabata duba da yanayin da ya samu mutanen Makka aciki na da ga tsatstsauran ruƙonsu ga gumaka, ya kwashi kimanin shekara uku a haka, kuma ya fi bada ƙarfi wurin kiran waɗanda ya

ke da kusanci da su, da ga cikin waɗanda suka bada gaskiya da shi akwai matarsa Kadija da amininsa Abubakar da ƙanin sa kuma agolansa Aliyu da kuma ƴantaccen bawansa Zai'du bini Sabit, Allah ya yarda da su gaba ɗaya, malamai sun yi saɓani game da wanda ya fara musulunta cikin waɗan nan bayin Allah, wasu suka rinjayar da cewa Abubakar ne farkon musulunta wasu kuma Kadija wasu kuma Aliyu, wasu kuma sun yi ƙoƙarin haɗa ruwayoyin da suka zo akan haka, suka ce farkon wanda ya fara musulunta acikin maza shine Abubakar a cikin mata kuma Kadija a cikin yara kuma Aliyu, wanda imam Abu Hanifa shi ya fara wannan jam'in kamar yadda Suyuɗi ya ambata acikin (Tarikul kulafa'a) ibni Kassir kuma ya rinjayar da cewa iyalan Annabi (saw) su suka fara musulunta, wato Kadija da Aliyu da Zai'du bini Sabit da ummu Ai'man da kuma Waraƙa bini Naufal, Al'malikul mu'ayyid, Abul Fida'i ya bai'yana a cikin littafinsa (Tariku Abil Fidai) cewa babu saɓani tsakanin malamai game da cewa kadija ce ta fara musulunta, wannan Magana ba haka ta ke ba, domin abin da na anbata maka da farko na saɓanin malamai, abu mafi inganci shine abin da imam Abu Hanifa ya tafi akan shi na yin jam'i kamar yadda ya gabata.

Haƙiƙa Abubakar ya bada gudummawa sosai wajen jawo ra'ayin wasu daga cikin manyan mutane zuwa ga musulunci, kamarsu Usmanu bini Affan da Abdurrahman bini Auf da Zubairu binil Auwam da sa'adu bini Abi Waƙƙas da Ɗalhatu bini Ubaidillah da sauran su.

## Darussan da ke cikin wannan darasin

1- Dukkanin al'amura ana binsu sannu sannu ne ba da garaje ba.
2- idan za ka fara da'awa ka fara daga cikin gida kafun ka fita waje.

3- Haƙiƙa iyalai nagari da abokanan kirki suna ba mutun gudum-muwa ƙwarai da gaske wajen tafiyar da lamuransa salin alin.

## Matakin da'awa a bayyane

Daga nan kuma sai aka umarci Annabi (saw) da ya fara da'awa a bayyane bayan jama'an da aka samu na da ga waɗanda suka yi imani da Allah, ayar da Allah ya saukar game da haka ita ce faɗin sa maɗaukakin sarki:

« وَأَنْذِرْ عَشِيرَتَكَ الأَقْرَبِينَ » الشعراء: (314)

Ma'ana: ka yi gargaɗi ga danginka makusanta.

Daga nan sai Annabi (saw) ya tara mutanensa ya hau dutsen Safa ya shiga yi musu gargaɗi, sai Abu Lahab ya mike ya ce da Annabi (saw) daman dan wannan ka taramu to yankewa, da halaka sun tabbata gareka a sauran kwanakinka! Sai Allah ya mayar masa da martani ta hanyar saukar da suratul Lahbi.

Daga nan Annabi (saw) ya ci gaba da kira zuwa ga Allah a bayyane a hankali a hankali mutane su na ganewa suna shiga cikin addinin Allah, yayin da ƙurai'shawa suka ga haka sai suka fara zuwa da ma-kirce makirce dan ganin sun dakushe hasken da'awar Annabi (saw) duk ba su ci nasaraba.

Musulunci ya ci gaba da haɓɓaka da burunƙasa mutane su na shiga Addinin Allah jama'a jama'a, su kuma manyan ƙurai'shawa suna nasu aikin na ƙoƙarin dakushe hasken wannan da'awa amma duk a banza, daga ƙarshe dai sai suka fito da wata hanya, wacce ta ke

ƙunshe da cutar da Annabi (saw) da musguna masa da kuma azabtar da duk wani wanda ya bada gaskiya da shi, yayin da ƙunci yai ƙunci cutarwa ta yi cutarwa, sai Annabi (saw) ya umarci wasu daga cikin sahabbansa da su yi hijira zuwa Habasha musammam masu rauni da ƙarancin galihu.

## Hijirar farko zuwa Habasha

Annabi (saw) ya na da masaniyar cewa Najashi sarkin Habasha na wannan lokacin adaline, saboda haka yayin da ya ga cutarwar ƙurai'shawa ga sahabbansa (ra) taƙici taƙi cinyewa sai ya umarcesu da su yi hijira zuwa ƙasar Habasha dan tsira da addininsu, hakan ya farune a cikin watan rajab a shekara ta biyar da annabci, sahabban da suka yi hijira a wannan lokacin su goma sha shida ne maza sha biyu mata huɗu, dukkanin su ƙarƙashin jagorancin Usman bini Affan tare da matarsa Ruƙayya ʿYar manzon Allah (saw)  wanda suka samu suka sulale cikin dare suka bi ta ɓarauniyar hanya don gudun kada ƙurai'shawa su cim musu, haƙiƙa sun samu kyakkyawar tarba wajen Najashi. A cikin watan Ramadan Annabi (saw) ya fito zuwa Harami a lokacin manya masu faɗa aji na ƙurai'shawa duk sun hallara, Annabi (saw) be yi wata wata ba ya karanta suratun Najami har ya zo kan faɗin Allah ta,ala:

« فَاسْجِدُوا لِلَّهِ وَاعْبُدُوا » النجم: (62)

Ma'ana: ku yi sujjada ga Allah kuma ku bauta masa.

Sai Annabi (saw) ya yi sujjada, yayin da ƙurai'shawa suka ji zancen Allah mai ɗauke da hikima da fasaha ya ratsa kunnuwansu kuma

suka ga Annabi (saw) ya yi sujjada, sai suma suka faɗi suka yi sujjada, wannan labarin ya isar ma sahabban da suka yi hijira zuwa Habasha sai suka yi tsammanin ƙurai'shawa sun musulunta, sai suka dawo zuwa makka, kafun su ƙarasa gaskiyar lamari ya bayyana garesu, wasunsu suka koma wasu kuma suka shiga, daga nan sai Ungulu Ta koma gidanta na Tsamiya, wato ƙurai'shawa suka ci gaba da azabtar da su sai ma abin da ya daɗu, da Annabi (saw) ya ga haka sai ya yi musu umarni da su sake yin hijira zuwa Habasha a karo na biyu, wanda adadin masu hijirar ya kai mutun ɗari da ʽYan kai maza tamanin da uku mata sha tara, da ga nan musulmai suka samu kwanciyar hankali da aminci suka ci gaba da bautar Allah salin alin, yayin da ƙuraish suka ga haka sai suka aika ma Najashi da mutun biyu da ga cikin wakilansu tare da kyaututtuka akan cewa waɗannan mutanen da suke zaune a wajenka mutanene da suka rabu da addininsu da suka gada iyaye da kakanni suka zo da wani sabon addini wanda ya saɓa da naka, saboda haka ka dawo mana da su, suka yi dai duk wani kitififi da bita da ƙulli amma daga ƙarshe ba su ci nasaraba najashi ya sa aka mayar musu da kyautarsu ya ƙara rungumar musulmai, da ga ƙarshe suka ƙara fito da wani makircin na cewa musulman nan da suke zaune a ƙasarsa ƙarƙashin kulawarsa addininsu ya saɓama naka, domin suna cewa Annabi isa (as) ba ɗan Allah bane, anan ne aka yi wannan shahararriyar muhawarar tsakanin Najashi da musulmai ƙarƙashin jagorancin Ja'afar bini Abi Ɗalib (ra) baffan Annabi (saw) wanda da ga ƙarshe Najashi ya gane musulmai sune akan gaskiya kuma ya ƙara girmamasu ya ci gaba da basu kariya, ƙasar sa ta zama mafaka garesu, ƙurai'shawa suka ƙara taɓewa da shiga cikin ruɗani.

Daga ƙarshe ma sai Najashi ya musulunta gaba ɗaya a yayin da ya gane cewa addinin Musulunci shine addinin gaskiya, har Annabi (saw) ya bada labarin mutuwarsa a lokacin da ya koma zuwa ga Allah ya kuma yi masa salatul ga'ib.

## Darussan dake cikin wannan marhalar ta da'awa

1- Babu wani abu a wannan Duniyar wanda zai tabbata ya tsayu da ƙafafunsa face sai ya haɗu da ƙalubale iri iri.
2- Haƙiƙa duk wanda ya ce zai bi tafarkin Allah ya yi ruƙo da shi gamgam to ya tanadi riga da wando da hula na haƙuri da juriya.
3- Abokan gaban addinin Allah ba za su taɓa sassautawa ba wajen ganin sun dusashedda haskensa.
4- idan gudanar da ibada ya gagari musulmi agarin da yake to ya yi ƙaura daga gareshi zuwa wurin da zai gudanar da ibada salin alin, wannan hukuncin ya na nan har izuwa tsayuwar ƙiyama.
5- a ko'ina akwai na Allah.
6- Adalci a cikin shugabanci ya na jawo hankulan mutane zuwa ga wan nan shugabancin komai nisan sa.
7- Faɗi tashin sahabbai wajen ganin wanzuwar Musulunci, wannan ya na bayyana falalarsu kuma yana bayyana cewa duk wani musulmin da ya ke ƙafafa da Musulunci a yau da gobe har izuwa tsayuwar ƙiyama to da bazarsu ya ke rawa.
8- Sannan wannan darasi ya ƙara futo mana da tsantsar tausayin Annabi (saw) da kuma jin ƙan sa ga sahabbansa (rah) ta yadda ya umarcesu da yin hijira zuwa inda zasu samu nutsuwa da kwanciyar hankali.

9- Babu laifi ga musulmi ya shiga cikin kariyar wanda ba musulmi ba a yayin buƙatar hakan, amma da sharaɗin kar hakan ya zamto ya taɓa wani abu na addininsa.

## Musuluntar Hamza baffan Annabi (saw) da Umar (rah)

Ana nan a wannan yanayin Allah ya azurta musulunci da wasu man-yan jigogi guda biyu, waɗanda su na da matuƙar kwarjini a idanun ƙurai'shawa, waɗannan mutane sune Hamza baffan Annabi (saw) da Umaru bini Kaɗɗab, haƙiƙa waɗanan matasa ne guda biyu waɗanda kowa ya na shayinsu ya na shakkarsu a cikin ƙurai'shawa, shi Hamza ya musulunta ne a shekara ta shida ta annabtaka, dalilin musuluntarsa watarana Abu Jahal ya zo wucewa ta wazen dutsen Safa, a lokacin Annabi (saw) ya na wajen, sai Abu Jahal ya sauke masa kwandan tijara da futsara ya masa ibar albarka irin ta su ta marasa mutunci tsofaffinƳan tasha manzan Allah (saw) bai ce masa kanzil ba, sai ya sa dutse ya fasa masa kai, to sai labari ya riski Hamza alokacin yana dawowa da ga farauta, cewa an ci zarafin ɗan ɗan'uwanka, sai ransa ya ɓaci daman gashi matashi mai ji da kansa, sai ya je ya sama Abu Jahal ya ce: ka ke zagin ɗan ɗan'uwana to ni ma ina kan Addininsa, sai ya buga masa bakan sa ya ji masa gagaru-min ciwo, da ga nan ya musulunta ya zamto gagarumar garkuwa ga musulmai.

Shi kuma Umar ya musuluntane bayan musuluntar Hamza da kwana uku, wanda gabanin haka Annabi (saw) ya yi masa addu'a ta shiriya, to watarana ya fito da takobinsa tsirara, sai wani ya haɗu da shi ya ce ina zuwa haka, sai ya ce zai je ya kashe Muhammadu ne (saw) sai ya ce to ya zaka yi da danginsa banu Hashim? Sai ya ce ina ganin kai ma ka karkace (ka musulunta) sai ya ce da shi ba na

nuna ma ka abin mamaki ba? ai ʽYar'uwakka da sirikinka duk sun musulunta, sai Umar ya tunkari gidan nasu a fusace, ya na isa ya tarar da Kabbabu ɗan Aratti a tare da su riƙe da wata takarda mai ƙunshe da suratu Ɗaha, yana karanta musu, yayin da ya ji motsin Umar sai ya ɓoye a cikin ɗaki ita kuma ʽYar uwar Umar ta ɓoye takardar, da ga ƙarshe dai abin da ya gudana ya gudana, bayan ya karɓi takardar ya karanta sai Allah ya kimsa masa san musulunci, ya musulunta musuluncinsa ya zama gagarumar garkuwa ga musulmai, abin da Da ba'a iya yinsa a fili aka zo ana yinsa a bainar jama'a.

## Yanke mu'amala da musulmai

A yayin da ƙurai'shawa suka ga duk wani makirci da ƙulle ƙullensu wajan ganin dakushe hasken musulunci da kange mutane ga barin shi ya ƙi yin tasiri, maimakon hakama sai daɗa haɓaka ya ke da burunƙasa, sai suka shiga mitin ɗin gaggawa dan nemawa kansu wani matakin da ya kamata su kuma ɗauka, da ga nan suka haɗu akan cewa za'a yanke duk wata mu'amala da banu Hashim da banul Muɗɗalib, domin gaba ɗayansu sun haɗu wajen ba Annabi (saw) kariya, muminan su da waɗanda ma basu musulunta ba, suka ce ba za su ƙara wata mu'amala da su ba har sai sun bada Annabi (saw) an kashe shi, suka rubuta wannan zaluncin nasu a takarda suka rataye ta a ka'aba, su kuma banu Hashim suka ƙi yarda da hakan, suka zauna a haka ba'a siya daga garesu kuma ba'a sayar musu har tsawon shekaru uku, suka galabaita matuƙa, ana nan a haka sai Hishamu bini Amru da Zuhai'ru bini Abi Umayya suka haɗu, Hisham ya ce da zuhairu: shin yanzu za ka yarda ka ci ka sha hankali kwace ahalin kawunnan ka suna cikin halin da ka ke gani? Daman Hisham ya kasance ya na kawo ma banu Hashim abinci a ɓoye, shi kuma

Zuhai’ru ɗa ne wajen Atika 'Yar Abdulmuɗɗalib, da ga ƙarshe dai waɗannan mutanen guda biyu su suka yi ƙoƙari wajen kawo ƙarshen wannan mataki na zalunci da ƙurai’shawa suka ɗauka akan banu Hashim bayan sun nemi taimakon Abul Buktari bini Hisham da Zam’atu bini Aswad da kuma Almuɗ’im bini Adiyi, Annabi (saw) da jama’arsa suka fito da ga wannan kullen da aka ƙaƙaba musu, aka warware wannan takardar, Annabi (saw) ya bada labarin cewa za su tarar Gara ta cinye duk wani abu da aka rubuta a wannan takardar face sunan Allah, a wata ruwaya kuma akasin haka, ayayin da ƙurai’shawa suka isa sai suka tarar da ita kamar yadda Annabi (saw) ya bada labari, amma duk da haka wannan bai sa sun yi imani ba sun gasgata shi.

## Darussan da wannan darasin ya ƙunsa

1- Kafurai ba za su taɓa barin musulmi ya yi addinin sa salin alin ba sai sun bi duk wata hanyar da za su bi su ga sun hanashi aiwatar da addininsa, kuma hakan ya na kasancewa gwargwadon damar da suke da ita, idan damarsu taƙarfi ce sai su yi amfani da ƙarfi, idan kuma ta makirci ce sai su yi amfani da makirci.
2- Tsananin ƙaunar da Abu Ɗalib ya ke nuna ma manzan Allah (saw) wanda ko iyayen sa na da rai abin da za su iya masa kenan, domin a wannan halin da suka kasance a ciki, ya kasance ya na umartar Annabi (saw) da kwanciya a kan shimfiɗarsa har sai ya bari kowa ya yi barci sai ya umarci wani da ga cikin 'Ya'Yansa da ya dawo shinfiɗar Annabi (saw) shi kuma ya koma tasa saboda gudun kar a kawo masa sumame.

3- Tsantsar zumunci da ʽYan'uwantaka irin na larabawa, ta yarda za su iya bada rayuwarsu gaba ɗaya wajen kare rayuwar ɗaya daga cikinsu.
4- a ko'ina ba a rasa na kirki.

## Shekarar baƙin ciki

A shekara ta goma da ga annabtaka Abu Ɗalib ya koma zuwa ga Allah maɗaukakin sarki, wanda hakan ya farune bayan fitowarsu da ga wannan kullen da aka ƙaƙaba musu na watanni shida, a yayin da mutuwa ta zo masa sai Annabi (saw) ya shiga har makwancinsa a lokacin akwai Abu jahal da wasu da ga cikin manyan mushirikan ƙurai'shawa a wajen sa, sai Annabi (saw) ya ce da shi: ya baffa ce: (la'ilaha illallah) kalmace wacce zan sanya ta zamo hujja a gareka awajen Allah ta'ala, sai Abu jahal da Abdullahi bini Abi Umayya suka ce da Abu Ɗalib: shin yanzu kana kyamar tafarkin Abdulmuɗɗalib, ba su gushe ba dai su na kwaɗaitar da shi akan ƙara ruƙo da addininsu na gado, har ya cika, duk da haka Annabi (saw) ya ce ba zai gushe ba ya na nema masa gafarar Allah matuƙar ba a hana shi ba, bai gushe ba ahaka har aya ta sauka aka hana yiwa duk wani wanda ya mutu ba a bisa tafarkin Allah ba istigfari, sannan Allah ya bayyana ma Annabi (saw) cewa shi ba ya iya shiryar da wanda Allah bai nufeshi da shiriya ba, amma duk da haka sai da Annabi (saw) ya roƙa masa Allah akan ya sauƙaƙa masa azaba agobe ƙiyama kuma Allah ya amsa, haƙiƙa Abu Ɗalib ya cancanci hakan daga Annabi (saw) domin soyyayar da ya nuna masa ta ma wuce ta ɗa da uba, kuma ya na ɗaya daga cikin manyan turakun da

suka ƙarfafi da'awar Annabi (saw) har ta kai inda ta kai, haƙiƙa acikin rashin musuluntarsa akwai wani ɓoyayyen sirri na Allantaka, wanda dole ayarda da shi.

Daga nan ba a jima ba sai sayyada Kadija (ra) ta koma zuwa ga rahamar Allah acikin dai wannan shekarar, da ga nan sai aka anbaci shekarar da suna shekarar baƙin ciki, haƙiƙa ta dace da wannan sunan, domin a cikinta ne Annabi (saw) ya rasa wasu manyan jigogi kuma masoya wanɗanda suka taka muhimmiyar rawa wajen kare Annabi (saw) da kuma ƙarfafar da'awarsa, haƙiƙa Annabi (saw) ya ji mutuwar waɗannan bayin Allan ƙwarai da gaske, da ga nan kuma sai ƙurai'shawa suka buɗe wata kasuwar rashin mutunci da musgunawa da cutarwa ga Annabi (saw) daman su na ragawa ne dan waɗannan mutanen guda biyu, to yanzu kuma babu su.

**Darussa:**

1- Haƙiƙa Allah ba ya barin wani dan wani, duk wanda ajalinsa ya yi to dolene ya tafi, da Allah ya na barin wani dan wani to da ya bar iyayen Annabi (saw) da matarsa Kadija (ra) da baffansa Abu Ɗalib.
2- Shiriya da ɓata duk a hannun Allah suke, shi ya ke shiryar da wanda ya so da falalarsa, ya ke kuma ɓatar da wanda ya so bisa adalcinsa da hikimarsa.
3- Allah ya na ƙarfafar addininsa ta hanyar wanda ba musulmi ba.
4- Addinin Allah bai rataya da gangar jikin wani mutum ba ta yadda za a ce yana mutuwa shima ya mutu, Allah shi ya ke gudanar da kayan sa.
5- An gina rai akan nuna damuwa da baƙin ciki bisa rabuwa da masoyi.

## Auren Annabi (saw) da Saudat

Bayan rasuwar sayyada kadija (ra) sai Annabi (saw) ya auri Saudat bintu Zam'at, wacce ta na ɗaya da ga cikin waɗanda suka yi hijira ta biyu zuwa Habasha, aciki har da mijinta Assukran bini Amru, wanda ya yi wafati acan, a wani ƙauli kuma bayan dawowarsa Makka, a yayin da ta gama takaba sai Annabi (saw) ya aureta, wacce ita ce mace tafarko da ga cikin matayen da ya aura bayan wafatin kadija (ra)

## Fara Da'awa a wajen Makka

Da ga nan sai Annabi (saw) ya fara fita wajen Makka ya na da'awa, daga cikin wuraren da ya fara zuwa akwai Ɗa'ifa, tazarar da ke tsakanin  sa da garin Makka tafiyar kilo mita sittin ne, haka Annabi (saw) ya yi takanas ta Makka zuwa Ɗa'ifa a ƙafarsa tare da'Yantaccen bawansa Zai'du binu Harisa, ya shiga ya na kiransu zuwa ga Allah Jalla wa'ala, ya na mai neman su ƙarfafeshi har ya isar da saƙon Allah, amma bai samu wata kyakkyawar Magana ba daga ɗayan su, bal maimakon haka ma sai suka cutar da shi suka sa wawaye suka masa atule suka jejjefeshi har suka fasa masa kai sai da jini ya gangaro har digadigansa, Zai'du binu Harisa ya kasance ya na kare sa wanda shi ma sai da ya samu raunuka, a yayin da waɗannan mutanen suka wulaƙanta Annabi (saw) sai Allah ya faranta zuciyarsa ta hanyar aiko masa da mala'ikan duwatsu, ya nemi zabin sa akan a darkake waɗancan mutanen da suka masa wannan tozarci, amma Annabi (saw) ya ce a  kyalesu wataƙila nan gaba Allah ya fitar da waɗanda zasu bautawa Allah a tsatsansu, sannan kuma Allah ya

ƙara faranta masa rai ta hanyar turo masa da runduna guda ta Aljanu waɗanda suka yi imani da Allah, don a kwantar masa da hankali a nunawa mutane idan sun ƙi yin imani da shi to Allah ya hore masa wata halitta wacce mutum bai isa ya ganta ba a surarta anan duniya amma shi Allah ya hore masa su.

**Darussa**

1- Shar'anta yin tafiya zuwa wani gari don yin da'awa da kira zuwa ga Allah.
2- Manzancin Annabi (saw) gamamme ne bai keɓanta da wasu mutane ba.
3- Babu wani abu mai mahimmanci a wannan Duniyar da za a samu cikin sauƙi ba tare da an yi faɗi tashi ba, haƙiƙa da Allah ya so kowa ya yi imani da Annabi (saw) ya ƙaunace shi ya karɓi abin da ya zo da shi na manzanci cikin sauƙi da ya yi haka, amma sai ya jarabe shi da mutane suka ƙi karɓar abun da ya zo da shi suka cutar da shi dan a nunawa na baya cewa babu wani abu da za a samu cikin ruwan sanyi koda kuwa ya na da alaƙa da addinin Allah, bal dole sai an sha wahala kafun a cimma gaci.
4- Tausayin Annabi (saw) da jinƙansa ga al'ummarsa.
5- idan wani ya ƙi ka da wuni to wani zai so ka da shekara, a yayin da mutanen Ɗa'if suka ƙi Annabi (saw) bal, suka kore shi da jifa da cim mutunci al'halin ya yi takanas ta Makka zuwa gare su, sai ga shi an samu Aljanu su kuma sun yi takanas ta wata uwa duniya zuwa gare shi tare da so da ƙauna, haka lamarin Allah ya ke.

## Isra'i da mi'iraji

a farko farkon shekara ta sha uku da ga Annabci wato gabanin hijira da shekara ɗaya, aka yi isra'i da Annabi (saw) da ga masallacin Harami zuwa masallacin ƙudus, kamar yadda imamul Harbi yai jazama da hakan, a wani ƙaulin kuma aka ce hakan ya faru a shekara ta biyar da ga annabci kamar yadda imamuz – Zuhuri ya yi jazama da hakan Nawawi ya inganta shi a cikin (Al'minhaj) sharhu muslim, amma zance mafi inganci shine abin da imamul Harbi ya tafi akan sa.

Al'israi a harshen larabci shine yin tafiya cikin dare, haƙiƙa an yi isra'i da Annabi (saw) da gangar jikin sa a bisa zance ingantacce, da ga masallacin Harami zuwa masallacin ƙudus akan wa ta dabba mai suna Buraka, bisa rakiyar Jibrilu (as) yayin da aka isa ƙudus sai Annabi (saw) ya yada zango ya jagoranci Annabawa (as) sallah ya ɗaure Burakar a bakin ƙofar Masallacin.

Da ga nan sai aka ɗauke shi zuwa saman Duniya a wannan daren, a yayin da aka isa sai Jibrilu (as) ya nemi a buɗe masa sai aka buɗe masa, sai Annabi (saw) ya ga Annabi Adam (as) baban mutane a sama ta ɗaya, ya yi masa sallama sai ya amsa masa sallamarsa ya yi maraba da shi ya kuma tabbatar da annabcinsa, sannan sai Allah ya nuna masa rayukan nagartattun mutane masu rabo da ga daman sa da na miyagun mutane marasa rabo daga hagunsa.

Sannan sai aka ɗauke shi zuwa sama ta biyu, Jibrilu ya nemi a buɗe masa, sai aka buɗe masa, sai Annabi (saw) ya ga Annabi Yahya ɗan

Annabi Zakariyya da Annabi Isa ɗan Maryam (as) sai ya musu sallama suka amsa masa suka yi maraba da shi suka tabbatar da annabcinsa.

Sannan aka hau da shi sama ta uku, sai ya ga Annabi Yusuf (as) a cikinta, sai ya yi masa sallama ya amsa masa ya yi maraba da shi ya tabbatar da annabcinsa.

Sannan aka ɗauke shi zuwa sama ta huɗu sai ga Annabi Idris (as) acikin ta sai Annabi (saw) ya yi masa sallama sai ya amsa masa ya yi maraba da shi ya kuma tabbatar da annabcinsa.

Sannan aka ɗauke shi zuwa sama ta biyar, sai ya ga Annabi Harun ɗan Imrana (as) a cikin ta, abin da ya gudana da sauran annabawan da ya gani ya gudana tsakanin shi da Annabi Harun (as)

Sannan aka ɗauke shi zuwa sama ta shida, sai ga Annabi Musa (as) a cikinta, sai Annabi (saw) ya yi masa sallama, sai ya amsa masa ya yi maraba da shi ya kuma tabbatar da annabcinsa, yayin da Annabi (saw) ya ɗan matsa gaba da annabi Musa (as) sai Annabi Musa (as) ya yi kuka, aka tambaye shi me ya sa ka kuka? Sai ya ce ina kukane saboda naga wani yaro wanda aka aiko daga bayana waɗanda za su shiga Aljanna a cikin al'ummarsa sunfi waɗanda zasu shiga Aljanna daga cikin al'ummata. Annabi Musa (as) ya faɗi hakane dan baƙin ciki bisa yadda al'umarsa banu Isra'ila suka bijire masa ba wai ya na wa Annabi (saw) hassada ba ne, Allah ya tsareshi da hakan.

Sannan sai aka ɗauki Annabi (saw) zuwa sama ta bakwai, sai ya haɗu da Annabi Ibrahim (as) a cikinta, sai ya yi masa sallama, sai ya amsa masa ya yi maraba da shi ya tabbatar da annabcinsa.

Sannan aka ɗaga shi zuwa magaryar tikyewa sai ga ƳaƳanta kamar tulunan garin Hajar (Hajar: wata alƙarya ce kusa da madina, wacce mazaunanta sun shahara da sana'ar haɗa tulu) sai ga ganyan ta kamar kunnuwan giwa, sannan sai wata shimfiɗa ta Zinariya ta lullußbe ta da wani haske da kuma wasu launuka, sai ta canza babu wani mahaluƙin da ya isa ya siffanta kyawunta.

Sannan sai aka nuna masa baitul Ma'amur, sai ga shi a kowace rana mala'iku dubu saba'in ke shigar sa kuma ba sa dawowa, sannan sai aka shigar da shi Aljanna sai ga waɗansu tuddai a cikinta waɗanda suke na lu'ulu'u ne kamar yadda ya zo a ruwayar Bukari, sannan kuma ƙasar ta ta Almiski ce, sai Annabi (saw) ya hau kan wani abun hawa wanda ya na jiyo sautin alƙalami da ga nan a yayin da ya ke rubutu.

Sannan sai aka ɗauke shi zuwa ga fadar Allah jalla wa'ala, ya kusanta da shi har ya kasance nisan da ke tsakaninsu kamar gwargwadon tsawon baka biyu ne, da ga nan sai Allah jalla wa'ala ya yi masa abin da ya yi masa na wahayi aka wajabta masa salloli hamsin shi da al'ummarsa, abin da ya faru tsakanin sa da Musa ya faru har ta dawo guda biyar tare da samun ladan guda hamsin.

Wannan lafazin Bukari da muslim ne, tare da cewa akwai wasu ƙare ƙare, haƙiƙa ruwayoyin da suka zo game da isra'i da mi'iraji su na da matuƙar yawa, wanda su na nan a cikin littattafan Hadisi na (Sunan) da (Sihah) da (Masanid) da (Ma'ajim) da wasunsu na da ga littattafan sunnah.

A yayin da Annabi (saw) ya ba ƙurai'shawa wannan labarin ya nuna musu duk wani abu wanda ya ke bayyana iyakar gaskiyarsa a cikin

wannan lamari, amma sai suka ƙaryata shi suka ƙara kafurce masa suka masa izgilanci, aka je aka samu Abubakar Assiddiƙ aka ce da shi ka ji abin da abokin ka ya ke faɗa, maimakon su ji ya ƙaryata shi sai ya ce: shi ya faɗa muku haka da bakinsa? Suka ce: eh, sai ya ce: to idan ya bada labarin abin da ya fi haka ma zan gasgata shi, da ga nanne aka masa laƙabi da (Assiddiƙ) wato mai yawan gasgatawa.

## Darussa

1- Haƙiƙa duk tsanani yana tare da sauƙi, a duk lokacin da Allah ya jarabci Annabi (saw) da wata jarabawa ta cutarwar abokan gaba, sai ya yi masa tagomashi da wata gagarumar kyauta wacce bai taɓa ma wani ita ba, a yayin da ƙurai'shawa suka tsananta cutarwarsu da tsiyatakunsu gareshi sai Allah yai masa wannan gagarumar ni'imar wacce babu wani mahaluƙin da aka taɓa masa kwatankwacin ta.
2- Haƙuri da juriya sune manyan jigogin da suke jagora zuwa ga cimma gaci.
3- Girman sha'anin Manzon Allah (saw) ta yadda Allah ya ɗaukaka sa akan dukkanin halittu ya taka maƙamin da ba wanda ya taɓa takawa ya je wurin da ba wani mahaluƙin da ya taɓa zuwa.
4- Mubaya'ar manyan annabawa gareshi, wannan ƙara lallashi ne zuwa gare shi da kuma kwantar masa da hankali, cewa idan ƙurai'shawa sun ƙi yin imani da shi, to ga wasu daga cikin manyan annabawa sun masa mubaya'a.
5- halaccin nuna damuwa saboda wani ya wuce ka da wani abu da ya ke da alaƙa da addini, kamar yadda Annabi Musa (as) ya yi, wannan ba ya daga cikin jerangiyar hasada wacce aka hana.

6- ƙarfin imanin Abubakar Assiddiƙ da kuma tatacciyar soyayyarsa ga Annabi (saw)

Haƙiƙa akwai fa'idodi masu tarin yawa a wannan darasi, amma littafin ba zai bada goyon baya ba wajen anbatarso duka don gudun tsawaitawa.

## Farawar Musuluncin Al'ansar da Al'Bai'atul Aƙabatu

a shekara ta goma sha ɗaya da ga annabci aka samu mutun shida daga cikin mutanen Madina suka musulunta a lokacin da Annabi (saw) ya bijiro musu da Musulunci lokacin aikin Hajji ne, ya karanta musu Kur'ani, da ga cikin babban abin da ya ɗauki hankulansu har suka musulunta, shine sun kasance suna zaune da yahudawa a wuri ɗaya, to idan wani abu na yaƙi ya haɗasu da su sai yahudawa su ce da su akwai wani Annabi da za a aiko nan ba da jimawaba kuma ya na bayyana za mu yi imani da shi mu bishi, mu haɗu da mu da shi mu yi muku irin kisan da aka wa adawa da Samudawa, to yayin da Annabi (saw) ya kira waɗannan mutun shida ɗin zuwa ga Allah sai suka ce da junansu lalle wannan shine annabin da yahudawa suke ba ku labarin zuwansa saboda haka ka da ku bari su rigaku yin imani da shi, sai suka yi imani da shi suka koma madina a bisa cewa za su dawo shekara mai zuwa, da suka koma sai suka kira mutanensu zuwa ga musulunci suka ba su labarin Annabi (saw) da al'amarinsa, sai mutanen Madina suka karɓi Musulunci har ta kai cewa babu wani gida da ga cikin gidajen Al'ansar face anbaton Manzon Allah (saw) ya shiga cikin sa.

Da shekara ta kewayo sai mutun goma sha biyu suka kuma zuwa daga Madina a cikin su akwai mutun biyar daga cikin mutane guda

shidan farko, sun zo ne dan ƙara jaddada mubaya’arsu ga Annabi (saw) suka same shi a wajen (Al’aƙabatu) suka yi masa mubaya’a akan cewa ba za su yi shirka da Allah ba, ba za su yi sata ba, ba za su yi zina ba, ba za su kashe ƳaƳayensu mata ba, ba za su kuma zo da ƙiran ƙarya ba ta kowace fuska, sannan ba za su saɓa ba a cikin sanannan abu ba na shara’a, Annabi (saw) ya ce idan ku ka cika wannan alƙawari to sakamakon ku shine Aljanna, idan kuma ku ka saɓa to al’amarin ku ya na ga Allah.

Yayin da za su koma gida sai Annabi (saw) ya haɗa su da Mus’ab ɗan Umair domin ya karantar da su addinin Allah, wanda ya sauka a gidan As’ad binu Zurara (ra)

A yayin da wata shekara ta kuma dawowa sai suka ƙara zuwa suka yi mubaya’a a wannan wurin dai a karo na biyu.

### Darussa

1- A yayin da na kusa da kai ya bijire maka akan abin da ka zo da shi na shiriya to a wannan lokacinne wani zai yi tattaki da ga wata uwa Duniya ya zo inda kake don karɓar wannan shiriyar.
2- Galibi mai da’awa na kusa da shi ba su cika karɓar abin da ya zo da shi ba na da’awa da ba shi muhimmanci.
3- Sau da yawa malami ya kan zama inuwar giginya, wannan ba abisa babinta take ba na zargi, kamar yadda ya ke a hausance, a’a wannan yabo ne gare shi zargi ne kuma ga mutanen da ke kusa da shi waɗanda ba sa anfana da shi, ma’anar malami inuwar giginya ce shine galibin waɗanda suke amfana da shi da ga nesa suke, amma sai ka ga na kusa da shi basa amfana da shi, a’a sai dai su tafi wata uwa Duniya, tare da cewa za a iya samun wasu

fa’idoji a tare da shi waɗanba ba lallai bane a same su awajen wancan da aka tsallake wannan aka je gareshi ba.

## Alamomin Hijira

Al’ansar sun ƙara dawowa sun jaddada mubaya’arsu a karo na biyu, Musulunci ya fara kafuwa a Madina, a yayin da ƙuraish suke ta shige da fice wajen cutar da musulmai da kuma daƙile cigaban Musulunci amma haƙansu bai cimma ruwa ba, sai Annabi (saw) ya fara umartar sahabbansa da yin Hijira zuwa Madina, sai suka fara shirye shiryen hijira, suka fara fita a ɓoye, farkon wanda ya fara isa madina shine Abu Salmata ɗan Abdul’asad.

A yayin da ƙuraish suka farga da hakan sai suka fara ƙoƙarin hana su hijira ta hanyar fito da salo daban daban, ko dai a raba miji da matarsa ko mata da mijinta ko ɗa da ubansa ko kuma a hana mutun tafiya da ko tsinke da ga dukiyar sa kamar yadda ya faru da Suhai’b Arrumi (ra) har sai da ya kasance cewa babu wani da ga cikin sahabbai a garin Makka face Annabi (saw) da kuma Abubakar da Aliyu (ram) wanda su ma sun tsaya ne bisa umarnin Manzan Allah (saw)

## taron ƙurai’shawa akan kashe Annabi (saw)

A yayin da ƙurai’shawa suka ga musulmai duk sun yi hijira zuwa Madina, kuma Musulunci ya kafu a can, sai suka kira taron gaggawa domin neman mafutar da zata kawo ƙarshen abin da ya zame musu ƙashin bakin tukunya shi bai shiga ba kuma bai fita ba kamar yadda suke riyawa, daga ƙarshe dai sai suka yanke shawara akan kashe Annabi (saw) gaba ɗaya akan cewa za su zaɓi zaƙwaƙwurin matashi a kowace ƙabila su haɗu su mai kwab ɗaya ta yadda banu Hashim ba za su iya yaƙarsu ba, wanda ya kawo wannan shawar shine Abu

Jahal Allah ya baƙanta fuskarsa, wanda wannan mitin ɗin ya farune a darun najawa, a ranar Alhamis ashirin da shida (26) ga watan Safar a shekara ta goma sha huɗu (14) da ga annabci.

To al'adar Annabi (saw) ya kasance ya na bacci bayan sallar isha'i har zuwa rabin dare, sannan sai ya fita zuwa masallacin Harami ya yi ƙiyamullai'li, to a wannan daren sai ya sa Aliyu ya kwanta a kan shimfiɗarsa ya lulluɓa da bargonsa, ya tabbatar masa da cewa wani mummunan abu ba zai same shi ba.

A yayin da dare ya tsala sai gungun waɗannan miyagun matasan da za su aiwatar da mummunan ƙudirin ƙurai'shawa akan Annabi (saw) suka yi cincirindo a kofar gidan Annabi (saw) suna jiran dare ya raba ya fito zuwa harami don ƙiyamullai'li sai su aiwatar da ƙudirinsu akansa, amma sai Allah jalla wa'ala ya ruguza wannan shirin nasu gaba ɗaya ta yadda ya ɗauke ganinsu da jinsu gaba ɗaya Annabi (saw) ya zo ya ratsa ta tsakiyarsu har ya watsawa kowannensu ƙasa a kansa ya na mai karanta faɗin Allah maɗaukakin sarki:

« وَجَعَلْنَا مِنْ بَيْنِ أَيْدِيهِمْ سَدًّا وَمِنْ خَلْفِهِمْ سَدًّا فَأَغْشَيْنَاهُمْ فَهُمْ لاَ يُبْصِرُونَ » يس: (9)

Ma'ana: sai muka sanya shamaki a gaba garesu da kuma baya garesu sai muka lulluɓe idanuwansu suka zamto ba sa gani.

Basu gusheba a haka su na dakon fitowar Annabi (saw) sai wani mutun wanda basu san shi ba ya zo ya ce me kuke jira haka, suka ce: Muhammad, ya ce: aikuwa kun taɓe kun yi asara ai ta nan gaban ku ya wuce har ya watsama kowannen ku ƙasa a kansa, har za su

tafi sai suka leƙa ta wata kafa da ke jikin ƙofar gidan Annabi (saw) suka ga Aliyu a kwance akan shimfiɗar Annabi (saw) lulluɓe da bargonsa, sai suka ce: wallahi wannan Muhammadu ne, sai Aliyu ya tashi daga kan shimfiɗar suka tambaye shi ina Annabi (saw) ya ke sai ya ce bai sani ba.

Annabi (saw) ya nufi gidan Abubakar Assiddiƙ daman Abubakar (ra) ya riga ya yi musu tanadin komai da komai, Abubakar ya tanbaye shi abin da ke faruwa, sai ya sanar da shi cewa an umarce shi da yin hijira, sai Abubakar ya tambayi Annabi (saw) ko ya na buƙatar rakiya ne? Ya ce: eh, Abubakar ya yi farin ciki da haka har sai da ya yi kuka, ya ɗauki hayar Abdullahi bini Uraiƙiɗ a matsayin madugu wanda zai nuna musu hanya, wanda ya kasance mushiriki ne daga ƙabilar banu Addail, su nana A'isha daƳar uwatta Asama'u (ra) suka shirya musu komai na daga abin da matafiyi ya ke buƙata, sai suka kama hanya har suka kai wani kogon dutse wanda ake kira da kogon Sau'ru, Abubakar ya ce kada Annabi (saw) ya fara shiga har sai shi ya fara shiga ya bincika ya tabbatar da cewa babu wani abu da zai cutar da Annabi (saw)

A lokacin da ƙurai'shawa suka samu labarin kuɓutar Annabi (saw) daga wannan tarkon nasu, sai hankalinsu ya kai ƙololuwar tashi suka shiga mitin ɗin gaggawa, daga ƙarshe suka sa tukuici mai tsoka ga duk wanda ya zo da Annabi (saw) da Abubakar (ra) a raye ko a mace, wanda yawan wannan tukuicin ya kai raƙuma ɗari (100) akan kowanne daga Annabi (saw) da Abubakar, dan da nan labari ya watsu cikin birni da karkara kowa ya na ƙoƙarin ya ga Annabi (saw) da Abubakar ya tafi da su zuwa ga ƙurai'shawa dan samun wannan

ladan mai tsoka, barada da jarumai da waɗanda suka ƙware ta fannin bibiyar sawu suka dinga neman Annabi (saw) da Abubakar ruwa ajallo, har suka kai wannan kogon da suka ɓuya aciki, suka dudduba ko za su ga Annabi (saw) da Abubakar (ra) amma sai Allah ya sanya shamaki a tsakanin su suka kasa ganin su, har Abubakar ya na cewa da Annabi (saw) da ɗayansu zai sunkuyar da kansa ƙasa da ya gan mu, Annabi (saw) ya ce: yi shiru ya kai Abubakar, me kake tsammani ace ga mutum biyu Allah shine na ukunsu, wanda akan shi Allah ya saukar da wannan ayar:

« إِلاَّ تَنْصُرُوهُ فَقَدْ نَصَرَهُ اللهُ إِذْ أَخْرَجَهُ الَّذِينَ كَفَرُوا ثَانِيَ اثْنَيْنِ إِذْ هُمَا فِي الغَارِ إِذْ يَقُولُ لِصَاحِبِهِ لاَ تَحْزَنْ إِنَّ اللهَ مَعَنَا فَأَنْزَلَ اللهُ السَّكِينَةَ عَلَيْهِ وَأَيَّدَهُ بِجُنُودٍ لَمْ تَرَوْهَا » التوبة: (40)

Ma'ana: idan ku ka ƙi taimakonsa to haƙiƙa Allah ya taimake shi a lokacin da kafurai suka fitar da shi daga garinsa a lokacin da Annabi (saw) da Abubakar kowannensu ya kasance ɗaya daga cikin biyu, a lokacin da suke cikin kogo, a yayin da Annabi (saw) ya ke cewa da Abubakar ka da ka damu lalle Allah ya na tare da mu (da taimakonsa da kulawarsa) sai Allah ya saukar da nutsuwa ga Abubakar ya ƙarfafa Annabi (saw) da wata runduna wacce ba kwa ganinta.

Daga nan Annabi (saw) da Abubakar suka ci gaba da zama a wannan kogon har tsawon kwana uku, Asama'u 'Yar Abubakar da ɗan uwanta Abdurrahman su na zuwa su na kawo wa su Annabi (saw) rahotannin abin da ya ke faruwa a ɓoye. bayan wutar neman Annabi (saw) da abokinsa ta ɗauke sai su Annabi (saw) suka fito daga kogon suka nufi Madina.

## Hijirar Annabi (saw) zuwa Madina

Annabi (saw) da abokinsa Abubakar (ra) suka kama hanya zuwa Madina Abdullahi bini Uraiƙiɗ na nuna musu hanya, wanda ya kasance masanin hanyane ƙwarai da gaske, ya dinga bi da su ta ɓarayin hanyoyi waɗanda ba kowa ya san su ba, haka dai suka yi ta tafiya, Abubakar Assiddiƙ (ra) ya na matuƙar taka tsantsan wajen kula da Annabi (saw) har ta kai wani lokaci idan suna tafiya sai ya bar wannan ɓarin ya dawo wannan ɓarin, Annabi (saw) ya tambaye shi dalilin haka, sai ya ce: ina jin tsoron kar wani ya kawo maka ha-rine, shi yasa idan ina ɓarinka na dama sai na ga kamar wani zai kawo maka hari ta hagu sai na dawo hagunka, haka ma akasin haka, ya kasance idan ana tafiya mutane suka ga Abubakar da Annabi (saw) sai su tambayi Abubakar wannan kuma waye gaba gareka? Saboda sun san Abubakar kasancewa ya na yawan bin hanyar dan fatauci saɓanin Annabi (saw) Sai ya ce wannan wani mutun ne wanda zai shiryar da ni ya ɗaurani akan hanya, sai su yi tsammani hanya ta zahiri ya ke nufi, haka dai tafiya ta ci gaba har suka kai Madina, wanda gabanin hakan abubuwa da yawa sun faru, na da ga ƙissar Suraƙa ɗan Maliku wanda ya so ya kawo ma su Annabi (saw) hari ya tafi dasu wajen ƙurai'shawa dan karɓar tukwuicin da aka sa ga wanda ya zo da su, amma sai haƙansa ya ƙi cimma ruwa ta yadda Allah ya nuna masa mu'ujizar Annabi (saw) ta yadda dokinsa ya ke maƙalewa a duk lokacin da ya kawo masu Annabi (saw) hari, amma idan ya fuskanci wata nahiyar daban sai ya yi tafiya cikin sauri da hanzari, da ga ƙarshe dai ya saduda ya mika wuya. Da kuma ƙissar zaman Annabi (saw) A ƙuba da gina musu masallaci da makamantan haka.

## Shigar Annabi (saw) Madina

Bayan Annabi (saw) ya zauna a ƙuba tsawon kwana huɗu ya assasa musu Masallacin ƙuba wanda shine farkon Masallacin da aka assasa akan tsoron Allah, sai Annabi (saw) ya yi sallah a cikinsa, sai ya ɗaga da ga nan ya nufi Madina wanda haka ya farune ranar Juma'a, sallar Juma'a ta riske shi a unguwar banu Salim bini Auf, ya yi mu su sallah wanda adadinsu ya kai su ɗari (100) daga nan sai ya tunkari Madina bisa rakiyar banu Najjar waɗanda suka kasance kawunnansa ne, suna rataye da takubban su, mutanen Madina suka yi tsinke don taryar Annabi (saw) suka cika da farin ciki domin basu taɓa ganin rana mafi alkai'ri ba irin wannan ranar ta zuwan Annabi (saw) suka yi ta tasbihi da tahmidi don nuna godiya ga Allah zahiri da baɗini, yaran su mata suka rera bai'toci suna masu ce wa: farin wata ɗan daren sha uku ya ɓullo mana, daga Saniyatul Wada'i (Makka) ya wajaba a garemu mu yi godiya ga Allah, mai kira ya na kira zuwa ga Allah, ya kai wanda aka aiko zuwa garemu, ka zo da al'amari wanda ake yi wa ɗa'a.

Al'ansar suka yi ta goggoriyo kowa ya na son Annabi (saw) ya sauka a gidansa, daga ƙarshe dai Annabi (saw) ya sauka a gidan Abu Ayyuba Al'Ansari.

### Darussa

1- A duk lokacin da maƙiya addinin Allah suka yi bita da ƙullensu wajen ganin sun dusashed da hasken Musulunci amma haƙansu ya ƙi cimma ruwa, to a ƙarshe matakin da za su ɗauka shine matakin kisa.

2- Mai da’awa ba zai taɓa rabuwa da ƙalubale ba na daga makirce makircen abokan adawar da’awarsa.
3- Duk yadda ka kai ga tsoron Allah da matsayi a wurinsa to ba za ka taɓa kuɓuta daga jarabawaba, domin duk halittun Allah ba mai daraja da girma kwatankwacin na Annabi (saw) a wajen Allah, amma ka ga irin jarabobin da Allah ya ke masa.
4- Haƙiƙa makircin abokan adawar addinin Allah ba zai iya dusashe hasken sa ba, bal da ga ƙarshe abin da ba sa son ya tabbata na burunƙasarsa sai ya tabbata.
5- Girman mu’ujizar Annabi (saw)
6- ƙarfin imanin Abubakar Assiddiƙ da kuma tsananin ƙaunar sa ga Annabi (saw) haƙiƙa in ka yi rantsuwa akan sakin aure akan cewa duk duniya ba wanda ya fi Abubakar (ra) son Annabi (saw) to rantsuwarka ba zata zartu ba, ma’ana matarka ba ta saku ba, domin ka duba yadda Abubakar ya ke fara gabatar da kansa zuwa ga haɗarurruka don kare rayuwar Annabi (saw) da ganin ya kuɓuta ko da shi zai halaka.
7- imanin mutanen madina da alherinsu ga almuhajirun da kuma tsananin nuna farin ciki da zuwan Annabi (saw)
8- Musulunci ba ya tabbata sai da daula mai ƙarfi ya na da ga cikin abin da ya sa Annabi (saw) ya yi hijira zuwa Madina.

# Da’awa  a Madina

Bayan Annabi (saw) ya tabbata a Madina ya gina Masallacinsa mai daraja, wanda ya na ɗaya da ga cikin waɗanda suka ba da gudu-muwa wajen gina shi da gangar jikinsu, sannan ya riƙi ɗakunan

matayensa a jikin Masallacin da ga gefensa, ya kuma gina babban waje wanda talakawan Muhajirai za su zauna a ciki kafun Allah ya hore musu su yi na su gidajen.

## ƙullaʽYan'uwantaka a tsakanin Muhajirun da Al'ansar

Da ga nan kuma sai Annabi (saw) ya shiga ƙullaʽYan'uwantaka a tsakanin muhajirun da kuma Al'ansar, wanda hakan ya faru ne a gidan Anas bini Malik

Wanda adadinsu ya kai casa'in (90) rabinsu Muhajirun rabinsu kuma Al'ansar kamar yadda ibnul ƙayyim ya bai'yana a cikin (Zadul ma'ad) haƙiƙa wannanʽYan'uwantakarʽYan'uwantakace mai ƙarfi ta yadda kowa ya na iya gadar ɗan'uwansa, haƙiƙa wannanʽYan'uwantakar ta misali ce wacce duniyar ɗan Adam ba ta taɓa shedar irinta ba, domin ba'ansare yakan raba gidansa da duk dukiyar da ya mallaka gida biyu ya ba abokin ɗan'uwantakarsa bamuhajire kashi ɗaya, kuma sai ya ba shi zaɓin mafi kyau da ga cikinta, kuma idan ya na da mata biyu sai ya ba shi zaɓin mafi kyawu da nagarta da ga cikinsu, sai ya saketa ya ba shi ita ya aureta, haƙiƙa wannan ʽYan'uwantakar tafi ƙarfin ta jini, domin ko a tarihi ba a taɓa jin kwatankwacinta ba gabanin lokacin sahabbai.

## Darussa

1- Musulunci addinine wanda bai taƙaita ba wajen shiryar da mutane zuwa ga sallah da azumi da ba da zakka da aikin Hajji ba kawai, a'a addinine wanda ya ke ƙoƙarin ganin gina alaƙa mai ƙarfi da so da ƙauna a tsakanin ɗaɗɗaikun musulmai da kuma gamayyarsu.

2- ƙarfin imanin Al'ansar da kuma amincewarsu ga Allah da manzansa, domin wannan abin da suka aikata na fifita 'Yan'uwansu Muhajirun daliline akan hakan.
3- Farkon abin da ya kamata mai da'awa ya fara yi bayan tabbatar da kyakkyawar aƙida a zukatan mabiyansa shine gina kyakkyawar alaƙa a tsakaninsu da kuma ganin sun zama 'Yan'uwan juna tsintsiya maɗaurin ki ɗaya.

## Tsarin zamantakewa da Yahudawa

Lokacin da Annabi (saw) ya zo Madina ya tarad da nau'in ƙabilu na Yahudawa guda uku, sune: banu ƙurai'za waɗanda gidajensu suke agefen Madina, da Banun-Nadir su ma gidajensu a gefen Madina suke, sai kuma banu ƙai'nuƙa'a, waɗanda gidajensu suke cikin ƙwaryar Madina, bayan waɗannan Yahudawan akwai kuma wasu shahararrun ƙabilu guda biyu sune Al'aus da Al'kazraja, su kuma mushirikaine a da, sune mafi yawancin Al'ansar waɗanda suka ƙarfafi Annabi (saw) to sun kasance gabanin zuwan Annabi (saw) ba sa ga Maciji, domin akwai yaƙi a tsakaninsu wanda ya haura shekara ɗari (100) kuma waɗannan Yahudawan da aka ambata a baya suna ba da gagarumar gudummuwa wajen rura wutar gaba a tsakaninsu, domin Yahudawa mutanene waɗanda suka kware wajen iya shirya makirci da ƙulle ƙulle da kitififi ta salo daban daban, shi yasa ma bayan Annabi (saw) ya haɗa kan waɗannan ƙabilu guda biyu sun zama tsintsiya maɗaurinki ɗaya, sai ya ƙulla alƙawarurruka da waɗannan Yahudawan akan a zauna lafiya ba tare da wani ɓangare ya cutar da ɗayan ɓangaren ba, ko kuma ya taimaki wani bare akan shi, sannan ya tabbatar musu da 'Yancinsu na 'Yan ƙasa, amma da ya ke mutanene fasiƙai fajirai ma'abota makirce makirce sai da

suka saɓa dukkan alƙawarurrukan, gini akan asalinsu gurɓatacce, wanda bayanin haka zai zo a mahallinsa insha Allah.

## Matakin kare kai

A yayin da ƙuraish suka ga daular Musulunci ta tsayu da ƙafafuwanta a Madina sai suka fara neman waɗansu hanyoyi na daban dan ganin bayan musulunci, suka rubutawa Abdullahi ɗan Ubayyu ɗan Salul wasiƙa akan ya yaƙi Annabi (saw) daman shi ya kasance mushiriki, kuma ana gab da naɗa shi sarki a Madina sai ga Annabi (saw) sai aka dakatar da wannan ƙudirin, to tun da ga nan ya fara neman hanyoyin da zai bi ya ga bayan Annabi (saw) yayin da ya ga wannan wasiƙar ta ƙurai'shawa sai ya yi nufin cika ƙudirinsu, amma bai ci nasara ba.

Duba da irin cutarwar da ƙurai'shawa suka yiwa Annabi (saw) da sahabbansa (ram) har suka fitar da shi daga mahaifarsa dan zalunci, kuma duk da haka ba su kyaleshi ba su na nan suna bin dukkan wasu hanyoyi waɗanda zasu ga bayansa da su, sai Allah jalla wa'ala ya yi ma sa izini akan mai'da martani ta hanyar yaƙar duk wanda ya kawo ma sa hari, da kuma cewa ces ga duk wanda ya ce masa kule, wanda ƙafun akai ga yaƙin Badar Annabi (saw) ya tura wasu daga cikin baradan sadaukan sahabbansa don kai wa fataken ƙurai'shawa hari akan hanyar su ta fatauci zuwa Sham, domin dole sai sun bi ta gefen madina, ya yi hakanne domin rage raɗaɗin zaluncin da ƙurai'shawa suka mu suna ƙwace dukiyoyinsu da matayensu da ƳaƳayensu, adadin wannan sumamen ya kai guda takwas, to da ga nan kuma sai babban yaƙi yaƙin Badar.

## Yaƙin Badar

Yaƙin Badar ya farune a sha bakwai ga watan ramadan a shekara ta biyu daga hijira (2) haƙiƙa yaƙin badar shine yaƙi mafi girma a tarihin Musulunci, wanda Allah ya ambaci ranar faruwarsa da ranar rabewa tsakanin ƙarya da gaskiya, ya ɗaukaka waɗanda ake ganin ƙasƙantattune akan manyan jagororin ƙurai'shawa waɗanda suke taƙama da mulki da dukiya, ya dakushe ƙarfinsu, (Badar) wani wurine wanda ya ke a tsakanin Makka da madina, amma ya fi kusa da Madina ƙwarai da gaske, akwai wata rijiya a wajen wacce ake kira da wannan sunan.

dalilin wannan yaƙin kuwa, shine Annabi (saw) ya samu labarin cewa ga fataken ƙurai'shawa nan dawowa da ga Siriya zuwa Makka, ƙarƙashin zagorancin Abu Sufyan, tare da su akwai raƙuma dubu (1,000) maƙare da himilin kaya na manyan ƙurai'shawa, wanda adadin kayan ya kai ƙimar dinari dubu Hamsin (50,000) kwatan kwacin nai'ra biliyon biyar da miliyon ɗari, wato nai'ra miliyon dubu biyar da miliyon ɗari (5, 100,000,000) a kuɗin mu na Naijeriya, a lissafin shekarar (1442) h, (2021) m, kuma waɗanda suke gadin dukiyar ba su fi mutun arba'in ba (40) yayin da mazan Allah (saw) ya samu wannan labarin sai ya kwaɗaitar da sahabbai akan su fito da shirin yaƙi dan fuskantar waɗannan fataken, wataƙila Allah ya sa su ɗan fanshe kaɗan daga cikin zaluncin da ƙurai'shawa suka musu na ƙwace musu dukiyoyinsu, wannan abin da Annabi ya yi ba fashi da makami bane kamar yadda abokan gabar Musulunci azzalumai marasa adalci suke yamiɗiɗi da shi, a a wannan ɗaukan fansane akan irin zaluncin da aka musu kamar yadda ya gabata.

Annabi (saw) ya fita wannan yaƙin tare da mayaƙan sahabbai (ram) wanɗanda adadinsu bai wuce ɗari uku da sha uku ba zuwa da sha

bakwai (313/ 317) tare da su akwai raƙuma saba'in (70) da kuma dawakai biyu (2) domin dayawansu ba su san cewa yaƙi za a yi ba, wanda mutun uku sukan haɗu akan raƙumi guda ɗaya su na yin hau in hau, wato idan wannan ya hau ya yi tafiyar wani ɗan zango da shi sai ya sauka wancan ma ya hau har suka isa filin daga, wato Badar.

Amma su kuma mushirikai adadinsu ya kai kusan dubu ɗaya (1000) tare da su akwai dawakai ɗari biyu (200) da kuma mata mawaƙa suna rera waƙoƙin ƙarfafa gwui'wa da kuma cin fuska ga musulmai.

Annabi (saw) ya jagoranci sahabbansa suka gaggauta kama wuri mafi kyau wato inda ruwa yake, daga nan sai Sa'ad ɗan Mu'azu ya nema daga Annabi (saw) akan a gina masa wani ɗan ɗaki wanda zai kasance a ciki ta yadda zai dinga bada umarni da ga nan, sai Annabi (saw) ya amince ya kuma yi wa Sa'ad fatan alheri, sai aka gina masa ɗan ƙaramin ɗaki akan wani ɗan tudu da ga arewa maso gabashin filin dagar, sannan Sa'ad ya sa aka zaɓo wasu daga cikin matasan Al'ansar don gadin manzan Allah (saw) a wannan ofis ɗin komandancin nasa.

A yayin da rundunonin biyu suka haɗu, sai Annabi (saw) ya shiga roƙon Allah ya na mai neman ya cika ma sa alƙawarin da ya yi ma sa na ba shi nasara akan abokan gabar Musulunci.

Annabi (saw) ya shiga shirya rundunar musulmai ya na daidaitasu sahu sahu, da ga nan sai Al'aswad ɗan Abdul Asad ya fito ya fara kirari ya na cewa sai ya kutsa har inda musulmai suke ya sha ruwan tafkinsu, wanda daman mutunne fasiƙi wanda babu alkai'ri a tare da shi, a yayin da yake wannan kirarin sai Hamza ɗan Abdul

Muɗɗalib yai fitar burgu ya na zuwa bai yi watawata ba ya kwashe ma sa ƙafafuwa da takobi kafun ya ƙarasa tafkin, amma duk da haka sai da kafurin ya rarrafa zuwa tafkin dan ya barrantar da rantsuwarsa, sai zakin Allah Hamza ya kara aiwatar da kansakalinsa a kansa, ya sheƙa barzahu.

Da ga nan sai aka fara fito na fito, inda aka samu Utbatu ɗan Rabi'a da ɗan uwansa Shai'ba da ɗansa Al'walid ɗan Utbatu, sun fito da ga ɓangaren kafurai, waɗanda dukkaninsu ƳYan gida ɗayane, a ɓangaren musulmai ma mutun uku suka fito daga cikin al'ansar, sune Auf da Mu'auwiz ƳaƳYan Al'haris, da kuma mahaifiyarsu Afra'u, sai waɗannan kafuran suka ce da su: ku kuma su waye? Sai suka ce mu Ansarawane, sai suka ce ba ku muke buƙata ba muna buƙatar tsararrakinmu ne, sai suka nema da ga Annabi (saw) akan ya fito musu da daidai da su, sai ya umarci Aliyu da Hamza da Ubai'da ɗan Haris manyan sadaukai dakarun Musulunci jarumai ba ku san tsoro ba, ba a je ko ina ba Aliyu ya sheƙar da Walidu ɗan Utba barzahu Hamza kuma ya sheƙar da Shaiba barzahu, aka yi kare jini biri jini tsakanin Ubaida da Utba, sai su Aliyu da Hamza suka kai sumame ga Utba suka aika da shi kushewarsa, suka ɗauki Ubai'da a yayin da aka yanke masa ƙafa ɗaya, wanda bai gusheba a haka har ya koma zuwa ga rahamar Allah jalla wa'ala.

Da ga nan kuma sai aka ruguntsume da yaƙi gaba ɗaya, bayan an yi wa arna gagarumar asara ta kashe musu manya daga cikin jigoginsu waɗanda suke ji da su, wanda hakan ya haifar musu da tsananinn baƙin ciki da kuma ƙara ƙulla mummunan ƙudiri akan musulmai, a yayin da aka fara wannan gagarumin yaƙin sai manzan Allah (saw) ya shiga roƙon Allah akan ya cika masa alƙawarin da ya yi

masa na samun nasara, ya kai matuƙa wajen ruƙon Allah ya na cewa: Allah in ka halakar da wannan ƙwaryaƙwaryan jama'a da ga yau baza a kara bauta maka ba, in ka so da ga yau ba za a kara bauta maka ba. har sai da mayafin Annabi (saw) ya faɗi Abubakar ya ma-yar masa da shi ya ce ya isa haka ya manzan Allah haƙiƙa ka nace akan ganin ubangijinka ya biya maka buƙata. yaƙi ya kai yaƙi.

Haƙiƙa Allah ya cika wa annabinsa (saw) alƙawarin da ya ɗaukar masa na nasara, domin ya ƙarfafi rundunar musulmai ta hanyar saukar da mala'iku waɗanda suka yi musharaka da musulmai a wannan yaƙin, Annabi (saw) ya fito da ga wannan ɗakin da aka tanadar masa yana cewa da sannu za a wargatsa taron abokan gaba su cikawa rigunansu iska su ari sawun kare, sannan sai ya ɗibi tsa-kuwowi ya fuskanci abokan gaba ya watsa mu su babu wani daga cikinsu face ta sameshi, shine Allah ya ke cewa: ba kai ka yi jifa ba a yayin da ka yi jifa, Allah ne dai kawai ya yi jifa.

wani da ga cikin mayaƙan musulmai ya na bada labari cewa, ya samu galaba akan wani arne ya na cikin ɗaure ƙafafunsa sai ya ji sautin bulala a samansa da sautin wani mahayi ya na cewa: zo ya kai Hai'zum, sai ya yi duba zuwa ga wannan mushirikin da ke gabansa sai ya ganshi ya faɗi ta rigingine, ya ga an tsaga hancinsa da fuskarsa Kaman shatin bulala, sai ya ba Annabi (saw) labarin abin da ya gani, sai ya ce da shi: ka yi gaskiya wannan ya na da ga cikin mala'ikun da Allah ya kawo mana agajinsu da ga sama ta uku, ha-kanan wani ba'ansare ya zo da Abbas ɗan Abdulmuɗɗalib a ɗaure, sai Abbas ya ce wallahi ba kai ka kamani ba wani mutunne da ga cikin mafi kyawun mutane wanda gashin kansa ya taƙaita a gefe da gefe haye bisa wani ingarman doki mai ratsin fari da baƙi shine ya

kamani, bam ma taɓa ganinsa ba, sai ba'ansaren ya ce: wallahi ni na kama shi, manzan Allah (saw) ya ce: yi shiru, haƙiƙa Allah ya ƙarfafeka da wani mala'ika mai karamci.

Ba a daɗe ba al'amari ya fara sham bambam, alamomin nasara suka fara bayyan ga musulmai alamomin watsewa suka fara tabbata ga mushirikai suka fara ja da baya suna gudu musulmai suka dinga binsu suna bigewa suna kamawa har suka kai ƙasa gaba ɗaya nasara ta tabbata ga musulmai.

Shi kuma jagoran rundunar mushirikai Abu Jahal, yayin da ya ga rundunarsa tana tambal tambal zata kife sai ya ƙara zaburar da jama'arsa, amma ina bakin alƙalami ya riga ya bushe, a yayin da aka samu wasu gwarazan sadaukan matasa guda biyu masu ƙarancin shekaru da ga cikin musulmai kowannensu yana tanbayar Abdurrahaman bini Aufi (ram) akan ya nuna ma sa Abu jahal, ya na cewa: An bani labarin ya na zagin Annabi (saw) wallahi idan mu ka yi tozali da shi to ba mai rabamu sai mutuwa, abun ya ba Abdurrahman mamaki, can sai ga Abu jahal, sai Abdurrahman ya ce dasu: ga mutuminku nan, sai kowanne da ga cikinsu ya yi fitar burgu suka masa kwab ɗaya suka aika da kafuri jahannama, suka juyo zuwa wajen Annabi (saw) kowanne daga cikinsu ya na cewa shi ya kasheshi, manzan Allah (saw) ya duba takubbansu sai ya ce ku biyu ku ka kasheshi, waɗannan samari sune Mu'azu ɗan Amru ɗan Jamuh, da mu'azu ɗan Afra'u (ram)

Allah ya cikama annabinsa alƙawarin da ya yi masa na nasara ya ɗaukaka Musulunci da musulmai a wannan yaƙin waɗanda a da su ake gani maƙasƙanta, ya kuma ƙasƙantar da manyan ƙurai'shawa

waɗanda a da ake gani maɗaukaka, musulmai suka shiga kama ribatattun yaƙi daga cikin mushirikai, wanda sai da suka kama mutun saba'in (70) da ga nan Annabi (saw) ya shiga neman shawarar sahabbansa (ram) akan me ya kamata a aikata da su, Abubakar (ra) ya bada shawarar a karɓi fansa da ga garesu domin Musulunci ya samu kuɗin shiga kuma a ƙara samun ƙarfin fito na fito da abokan gaba, Umar (ra) kuma ya bada shawara akan a sare musu wuya kawai, kowanne da ga cikin musulmai a ba shi ɗan uwansa kafuri ya aikata masa hakan dan kar ma wani ya ƙullaci wani akan ya kashe masa ɗan'uwa, Annabi (saw) ya karɓi shawarar Abubakar (ra) aka amshi fansa a wajensu, wanda adadin abin da aka sanya musu ya na farawa daga Dirhami dubu uku (3000) zuwa dubu huɗu (4000) wanda bai da kuɗi kuma sai a ba shi yara goma daga cikin yaran Madina ya koya musu karatu da rubuto irin wanda ake anfani da shi a wannan lokacin, har su iya, idan suka iya to ya fanshi kansa.

Washe gari sai Umar ya zo ya tarar da Annabi (saw) da Abubakar (ra) suna zaune suna kuka, sai Umar (ra) ya ce me yasa kuke kuka ya Manzan Allah? Idan kuka ya zo min sai nima na tayaku, idan kuma bai zo ba sai na ƙaƙalo shi, Annabi (saw) ya ce: ina kuka ne saboda shawarar da mutanenka suka bani akan karɓan fansa, haƙiƙa  an bijiro min da azabarsu mafi kusa da wannan bishiyar da ke kusa dani, domin ƙin karɓar shawararka, (wannan ba ya na nufin za a azabtar da waɗanda suka bada shawarar karɓar fansa bane, a a ana zarginsu ne akan haka)

Mutun goma sha huɗune (14) suka yi shahada da ga cikin musulmai a wannan yaƙin, a yayin da aka kashe mutun saba'in (70) daga cikin mushirikai, aka kama saba'in (70)

**Darussa**:

1- Musulunci ba ya goyon bayan musulmi ya zauna ayi ta cutar da shi, a a aduk lokacin da tsanani ya yi yawa cutarwa ta wuce gona da iri to anan ne matakin kare kai zai fara aiki, matuƙar akwai damar hakan, Annabi (saw) ya na cewa: ba a cizon mumini a rami sau biyu, ma'ana ka sa hannu a rami sai maciji ya sare ka ko wani ƙwaro ya cijeka sai ka kuma mayarwa ka ce bari in ji meke cikin ramin nan, wannan ba ɗabi'a bace ta mumini, wannan ba kuma ya na kore haƙuri ba ne, a a ba a ce mutun ya zauna ayi ta cutar da shi ba kuma yana da ikon kare kansa.
2- Jihadi shine ƙashin bayan addinin Allah, wanda ba ya tabbata sai da shi.
3- Sau dayawa ba a zama lafiya sai an zubar da jini tare da cewa zubar da shi ba alheri bane, amma wani lokaci yana zama alheri, domin in ba haka aka yi ba ba za a zauna lafiyaba.
4- Aduk lokacin da za afuskanci wani abu mai haɗari, to shugaba ya kamata ya kasance gaba gaba kamar yadda Annabi (saw) ya ke kasancewa gaba gaba a kowane yaƙi daga cikin yaƙoƙinsa.
5- Jarumtakar Annabi (saw) ta yadda ya taka gagarumar rawar gani a wannan yaƙin.
6- ƙarfin imanin sahabbai da kuma jarumtakarsu da sadaukan-takarsu, wanda ba dan su ba da wannan addinin bai zo manaba.
7- Yana da kyau shugaba ya kasance mai hikima da basira domin zaɓarwa jama'arsa abin da zai kai su ga cimma gaci, haƙiƙa mun ga ƙwarewar Annabi (saw) ta wajen iya tsara rindina da shiryar da su zuwa ga hanyar samun nasara akan abokan gaba.

8- Yana da kyau ga shugaba ya kasance mai neman shawarar talakawansa, koda kuwa ya taka kowane irin matsayi ta fuskar ilimi da hankali da hangen nesa, domin ba wani shugaba da ya kama ƙafar Annabi (saw) ta wannan janibin, amma tare da haka yana neman shawarar sahabbansa kuma ya yi aiki da ita.
9- Wannan yaƙin ya ƙara tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (saw) ta yadda abubuwa daban daban na mu'ujizozin da suka faru da kuma yadda Allah ya ɗaukaka gaskiya akan ƙarya.
10- A ƙarshen al'amari gaskiya ita ta ke yin galaba akan ƙarya, koda a farko ƙarya ta yi galaba akanta, to daga ƙarshe gaskiya zata koma sama ƙarya ta koma ƙasa, ko ma ta shafe gaba ɗaya.
11- Falalar Umar ɗan Kaɗɗab (ra) ta yadda Allah ya goyi bayan shawararsa ya zargi musulmai akan ƙin karɓarta, wannan ba shi bane karon farko da Alkur'ani ya ke goyon bayan maganarsa.
12- Halaccin musulmi ya koyi ilimi awajen kafurai, musamman idan ba wanda ya ƙware akan wannan ilimin da ga cikin musulmai, amma sai an yi taka tsantsan da gurɓatacciyar aƙidarsa.

## Yaƙin banu ƙai'nuƙa'a

Idan mai karatu bai mantaba mun ce daga cikin mutanen da Annabi (saw) ya tarar a Madina akwai Yahudawa, kuma sun kasu zuwa ƙabilu uku, wato: banu ƙurai'za, da banun-Nadir, da banu ƙai'nuƙa'a, kuma mun bayyana maka cewa Annabi (saw) ya ba su cikakken 'Yanci a matsayinsu na 'Yan ƙasa, bisa yarjejeniyar ba za su yi wa Musulunci wani zagon ƙasa ba, to amma da yake an baka labarin cewa su mutanene waɗanda suka yi ƙaurin suna ta wajen iya ƙulla makirci da annamimanci da yaudara da cin amana da saɓa

alƙawari, wannan bai ba su goyon baya ba wajen cika wannan alƙawarin da kiyaye wannan yarjejeniyar.

Shi wannan yaƙin ya farune a shekara ta biyu bayan hijira, sababin sa kuwa shine a yayin da yahudawan ƙai'nuƙa'a suka ga irin nasarar da Allah ya ba musulmai a Badar, sai wannan ya tayar da hassadarsu da baƙin cikin su, suka shiga ƙullawa musulmai makirce makirce daban daban, suna cutar da duk musulmin da ya gibta ta kasuwarsu, domin suna zaune ne a ƙwaryar birnin Madina, kuma sune mafi ƙarfi da arziki fiye da sauran ƙabilun Yahudawan da ke zaune a Madina, domin maƙera ne, suna ƙera tukwane da sauran kayan anfani na yau da kullun, shi yasa ma suka mallaki cikakkun kayan yaƙi, da Annabi (saw) ya ga haka sai ya tarasu ya yi musu nasiha, amma da yake zukatansu a ƙeƙashe suke wane dutse, sai suka fara cika baki suna cewa: ya Muhammadu kada kaga ka yi galaba akan ƙurai'shawa waɗanda ba su saba da gogayya ba basu san komai ba a ilimin yaƙi, in da da mu ka kara da kasan ka haɗu da majajen gaske sadaukai jarumai.

Sai shegantakar su taci gaba da daɗuwa, yau idan sun kunno waccan fitinar, gobe sai su takalo waccan, har takai wani bayahude ya kwance ma wata musulma zani a kasuwar  su tana mikewa sai ya faɗi suka yi ta dariya, sai wani musulmi ya zabura kansa ya kashe shi sai su kuma yahudawan suka tasamma sa da bugu har suka kasheshi, sai su kuma 'Yan'uwan wannan musulmin suka nemi ɗaukin 'Yan'uwansu musulmai, sai faɗa ya kaure, abubuwa marasa kyau suka faru.

A yayin da labarin wannan fajircin na su ya isa kunnen Annabi (saw) sai ya haɗo gangamin sojojinsa na sahabbai (ram) suka tsare su a cikin ganuwarsu har tsawon kwana goma sha biyar (15) daga ƙarshe Annabi (saw) ya kore su daga Madina gaba ɗaya kuma kada su maƙobce ta, kuma ba a yarje musu ɗaukan wani abu ba na daga dukiya sai dai matansu da 'Ya'Yansu kawai, Abdullahi bini Ubayyu bini salul ya yi iyakacin magiyar da zai iya yi akan Annabi (saw) ya kyale su amma bai saurareshi ba, Annabi (saw) ya raba dukiyarsu ga musulmai.

## Darussa

1- Haƙiƙa duk wanda ya bawa bayahude amana ko ya ƙullah alƙawari da su to baza a rabu lafiya ba.
2- Duk inda bayahude ya zauna tare da musulmi to sai ya yi amfani da duk wata hanyar da zata taimaka masa wajen ganin bayan wannan musulmin.
3- Fajircin yahudawa da kuma sharrinsu, haƙiƙa ba wani addini da mabiyansa suka kai yahudawa sharri da rashin alkairi.
4- ƙarshen mara cika alkawari taɓewa da nadama.
5- Ya halatta ga shugaba ya azabtar da azzalumi ta hanyar ƙwace masa dukiya.

## Yaƙin Uhudu

Uhdu wani dutsene daga cikin duwatsun Madina wanda Annabi (saw) ya ke cewa game da shi: wannan dutsen ya na son mu muma

muna sonsa. An kira shi da Uhudu ne saboda kaɗaituwarsa ga barin maƙobtaka da wani dutse, shi kuma yaƙin an ambace shi da wannan sunanne saboda ya farune a wajen da dutsen ya ke, sannan ya farune a shekara ta uku da ga hijira.

dalilin wannan yaƙin shine neman ɗaukan fansa, domin idan ba a mantaba a yakin Badar an cusama ƙurai'shawa baƙin ciki da takaici ta yadda aka kashe musu manyan jigoginsu waɗanda suke ji da su, irinsu Abu Jahal da Utba bini Rabi'a da ɗan uwansa Shai'ba da ɗansu Alwalidu ɗan Utba da makamantansu, da kuma yadda aka kama mutun saba'in da ga cikinsu a matsayin ribatattun yaƙi, wanda wannan ya ƙara rura gagarumar wutar gaba da ƙiyayyar Annabi (saw) da sahabbansa a zukatan su.

Sai manyansu suka shiga mitin dan neman hanyar da za abi a ɗauki fansa, ƙarƙashin jagorancin Abu Sufyan da Ikramata ɗan Abu Jahal da Sufwan ɗan Umayya da Abdullahi bini Abi Rabi'ata, suka fama wa mutanensu tsohon raunin da aka musu a yaƙin Badar na kashe musu iyaye da ƳaƳa da ƙannai da Ƴan'uwa, sai suka tara musu dukiya gami da dukiyar da ta kuɓuta a yaƙin Badar domin yaƙar musulmai, suka yi gagarumin shiri, wanda adadinsu ya kai dubu uku (3000) suka fito har da matayensu dan su ƙara musu ƙwarin gwui'wa, a tare da su akwai raƙuma dubu uku daidai da adadinsu da kuma dawakai ɗari biyu (200) da sulke ɗari bakwai.

A yayin da labari ya riski Annabi (saw) cewa ga ƙurai'shawa nan sun yi gagarumin shiri sun tinkaro Madina, dan da nan Annabi (saw) ya shiga neman shawarar sahabbai (ram) shin ya je ya taryesu ko kuma ya jirasu a Madina? Shi Annabi (saw) a ra'ayinsa kada a fita a tarye

su, a a ayi ganuwa a Madina idan suka shugo a yaƙe su, amma sai gwarazan mayaƙan sahabbai suka bada shawarar a fita a tarye su kamar yadda aka yi ayaƙin Badar, annabi (saw) da sahabbai suka yi zaman dako su na jiran zuwan abokan gaba, aka baza yan leƙen asiri a hanyar da ake ganin abokan gaba za su ɓullo ta cikinta.

Adadin musulmai a wannan yaƙin ya kai dubu ɗaya (1000) a yayin da suke da Doki ɗaya kacal sai kuma sulkuna (rigunan ƙarfe waɗanda ake sawa a yayin yaƙi dan kariya daga sara ko suka) guda ɗari (100)

Annabi (saw) ya ba sahabbai labarin cewa ya ga wata yar kafa a jikin takobinsa a mafarki, sannan kuma ya ga an yanka wani sa, sannan kuma ya ga ya shigar da hannunsa cikin wani sulke mai ba da kariya, sai ya fassara wannan kafar da aka nuna masa a jikin takobinsa da cewa zai rasa wani da ga cikin manyan makusantansa, wannan kuma San da aka yanka wasune daga cikin sahabbansa za su yi shahada, wannan kuma sulken kuma Madina ce.

Annabi (saw) ya tsara rundunarsa ya karkasa su zuwa gida uku: rudunar Muhajirai, da ta Al'aus daga cikin Al'ansar, da kuma ta Al'kazaraj suma daga cikin Ansarawa, sannan ya rarrabawa kowane ɓangare tutarsa, sannan ya zaɓi gwaraza ƙwararru wajen iya harbi guda hamsin (50) ƙarƙashin jagorancin Abdullahi bini Jubair ɗan Nu'umanu Al'Ansari Al'ausi, ya umarcesu da su tsaya akan wani dutse ka da su sauka, sawa'un musulmaine da nasara ko kuma akasin haka.

Akan hanyane aka samu wasu munafukai ƙarƙashin jagorancin shugabansu ɗan Salul suka juya suka ce akan me za mu je a kashemu a banza! Wanda adadinsu ya kai ɗari uku (300) wato yawan musulmai ya ragu zuwa ɗari bakwai (700)

Haƙiƙa Abdullahi ɗan Haram mahaifin Jabir (ram) ya yi ƙoƙari wajen ganin ya shawo kansu amma bai ci nasaraba saboda wanda ya yi nisa ba ya jin kira.

A yayin da musulmai suka iso filin daga sai rundunonin guda biyu suka kacame da gagarumin yaƙi kowane ɓangare ya na ƙoƙarin ya ga bayan ɗayan ɓangaren, sahabbai suka dinga nuna ƙwarewarsu da jaruntakarsu suka yi bala'i kyakkyawan bala'i, sai Allah ya bawa musulmai nasara akan abokan gabansu suka juya da baya suka cikama wandunansu iska.

A yayin da maharbannan suka ga wannan nasarar sai suka sakko daga kan wannan dutsen suka fara kwasar ganima alhalin Annabi (saw) ya ce ka da su sake su sakko, sawa'un musulmaine da nasara ko kuma akasin haka, wanda in da sunsan abin da zai biyo baya da ba su sakko ba, domin ma'aunin yaƙine ya juya al'amura suka rincaɓe ta yadda mushirikai suka yi anfani da wannan damar suka juyo suka kawo musu sumame, musulmai dayawa suka yi shahada.

Hamza ɗan Abdulmuɗɗalib baffan manzan Allah (saw) ne kamar yadda ya gabata, kuma ƙari akan haka ɗan'uwansa ne na shayarwa, haƙiƙa ya yi gagarumar rawar gani a yaƙin Badar ta yadda ya yi sanadiyar mutuwar jigajigan ƙurai'shawa waɗanda ake ji da su, kamar yadda hakan ya faru a wannan yaƙin, to duba da irin giɓin da ya yi ma ƙurai'shawa sai wannan yasa dayawa daga cikin waɗanda

ya kashe musu ƴan'uwa a Badar suka sha alwashin ɗaukan fansa, to Jubai'ru ɗan Muɗ'im ya na daga cikin irin waɗannan mutanen, domin an kashe masa ƙanin mahaifi a Badar (wato baffansa) to yana da wani bawa mai suna Wahshi, sai ya yi masa albishir da cewa matuƙar ya kashe Hamza a wannan yaƙin na Uhdu to ya ƴanta shi, sai ya fito tare da rundunar mushirikai dan aiwatar da wannan kudurin  na Jubair, a yayin da Hamza yake ta gididdibar mushirikai ya na sheƙar dasu barzahu, domin shi ɗaya ne tamkar da dubu, duk inda ya sa gabanshi sai dai ka ga kafurai suna zubewa ƙasa matattu kamar ana sassabe a gona, yana nan a haka shi kuma Wahshi ya dinga bibiyarsa yana seta shi da mashi, har ya tabbatar da lallai idan ya harbeshi da shi zai same shi sai ya sakar masa shi ya sameshi a mara har sai da mashin ya fito ta tsakanin cinyoyinsa, shi kuma za-kin na ka sai ya zaburo kan Wahshi amma ina, dafin mashin ya riga ya gama ratsa jikinsa kawai sai ya faɗi, shi kuma Wahshi bai cire mashinsa ba sai da ya ga ya mutu sannan ya je ya zareshi ya kama gabansa, daman shi ba yaƙi ya kawo shi ba kawai ya zo ne dan ya cika umarnin mai gidansa shi kuma ya ƴantashi, wanda da ga ƙarshe ya musulunta, amma yayin da ya zo karɓar musulunci wajen Annabi (saw) bai ba ri sun haɗa fuska ba saboda jin ɗacin abin da ya yi masa na kashe masa ɗan'uwa rabin jiki wanda yake ji da shi.

haƙiƙa mutuwar Hamza ba ƙaramin giɓi bane ga musulmai, kuma babban tabo ga Annabi (saw) wanda bai ɓace ba har ya koma zuwa ga Allah jalla wa'ala, domin Allah ya jarabci Annabi (saw) da sonsa ƙwarai da gaske, hakanne ma yasa annabi (saw) ya yi alwashin ɗaukan fansa. A yayin da ya cika sai Hindu yar Utba ta keta cikinsa

ta ciro hantarsa ta tauna ta furzar domin ta barrantar da rantsuwarta, kafurai suka yi masa musla, wannan shine ma'anar mafarkin da Annabi (saw) ya yi na ganin wata kafa a jikin takobinsa.

Haƙiƙa Abubakar da Umar da Aliyu da Zubai'ru da Mus'ab da makamantansu (ram) sun taka gagarumar rawar gani a wannan yaƙi sun yi ko a mutu ko ayi rai, sun yi ma mushirikai gagarumar ɓarna.

Haƙiƙa saukar maharban nan daga kan dutse ya haifar da abu mara daɗi, domin musulmai dayawa sun yi tsammanin yaƙi ya ƙare ne, sai suka yi sakwa sakwa suka rarraba su kuma kafurai sai suka yi anfani da wannan damar suka kawo musu mamayar ba zato, da ga nan kuma sai komai ya lalace al'amura suka rincaɓe, har takai ga mushirikai suka samu damar yi wa manzan Allah (saw) zobe, Abdullahi bini Shihab ya fasa masa kai, Utuba bini Abi Waƙƙas ya karya masa haƙori, Abdullahi ɗan ƙam'ata ya sare shi da takobi a kafaɗa amma ba tai nasarar huda sulkensa ba, ya kuma saransa har sai da turaku biyu daga cikin turakun hular ƙarfensa suka lume a muƙamuƙinsa, ya ce da shi: karɓa nine ɗan ƙam'atu, manzan Allah (saw) ya ce: allah ya tattaraka ya halakar da kai, Allah ya amsa addu'arsa, domin wata rana ya fita kewayen tumakinsa sai ya gansu akan ƙololuwar datse sai ya hau, sai wani rago ya tunkure shi ya faɗo ya dagargaje.

Daga nan sai Annabi (saw) ya yi wa ƙurai'shawa mummunar addu'a, ya na ayyana sunayen wasu da ga cikinsu ya na la'antarsu, sai Allah ya saukar da faɗinsa maɗaukakin sarki:

« لَيْسَ لَكَ مِنَ الأَمْرِ شَيْءٌ أَوْ يَتُوبَ عَلَيْهِمْ أَوْ يُعَذِّبَهُمْ فَإِنَّهُمْ ظَالِمِينَ » آل عمران: (128)

Ma'ana al'amarin shiryarwa da ɓatarwa ba a hannunka yake ba, kodai Allah ya gafarta musu ko kuma ya azabtar da su, domin tabbas su azzalumaine.

Bayan wutar yaƙi ta tsagaita sai Abu Sufyan ya hau kan dutse ya shiga kiran musulmai yana cewa: shin Muhammadu yana nan a cikinku? Sai Annabi (saw) ya ce: ka da wani ya ba shi amsa, sai ya kuma cewa: a cikinku akwai ɗan Abu ƙuhafa? (Abubakar) ba wanda ya ba shi amsa, sai ya kuma cewa: a cikinku akwai Umar ɗan Kaɗɗab? Nan ma ba wanda ya ba shi amsa, sai ya ce: haƙiƙa waɗannan an gama da su, to a wannan lokacinne Umar ya kasa tanƙwara kansa ya mayar masa da martani ya ce: ya kai makiyin Allah duk waɗannan da ka ambata suna nan a raye haƙiƙa Allah ya wanzar da abin da ya ke baƙanta maka rai, domin dalilin da ya sa Abu Sufyan ya keɓance waɗannan mutanen guda uku da Ambato, shine ya san cewa sune ginshiƙan addini. sannan sai ya shiga yiwa gumakansu kirari yana cewa: ƙara ɗaukaka Hubal, sai Annabi (saw) ya ce: baza ku ba shi amsaba? Sai suka ce me zamu ce? Sai ya ce: ku ce: Allah shine mafi girma da ɗaukaka. Sannan sai ya sake cewa: mu muna da Al'uzza (ɗaya daga cikin gumakansu) ku kuma ba ku da shi, sai Annabi (saw) ya ce: ba zaku ba shi amsaba? Suka ce: me zamu ce: ya ce: ku ce Allah shine majiɓincinmu wanda yake mana jagora a dukkan lamuranmu ku kuma ba ku da wanda ya ke jiɓintar lamuranku, sannan sai Abu Sufyan ya kuma cewa: wannan ranar a wajan

mu kamar ranar badar ce a wajan ku, shi kuma yaƙi daman watarana yakan zo maka da nasara watarana kuma ya zo maka da akasin ta.

Adadin waɗanda Allah ya azurta da shahada a wannan yaƙin ya kai saba'in (70) Annabi (saw) ya yi umarni da abinnesu a cikin tufafinsu da jininsu ba tare da an yi musu wanka da sallaba, wannan ya nuna shi shahidi na filin daga ba ayi masa wankan gawa da sallah, ba kuma abinnesu a cikin tufafin da ba nasu ba, wannan ita ce maz'haba ingantacciya wacce dalilan shara'a suke goyan bayanta, ya tabbata a cikin Sahih na Al'imamul Bukari hadisin Uƙubatu ɗan Amir, cewa Annabi (saw) ya yi musu sallah bayan shekara takwas (8) to amma wannan ba sallah bace wacce aka sunnanta yiwa gawa, a,a sallah ce ta bankwana da neman gafara, kamar yadda zahirin siyaƙin hadisin ya nuna, domin hakan ya farune a shekarar da Annabi yai bankwana da Duniya ya koma zuwa ga rahamar Allah.

Daga nan Annabi (saw) ya koma gida Madina, wanda a wannan lokacinne tsantsar soyayyar da sahabbai (ram) suke ma sa ta ƙara bayyana, domin akwai wata baiwar Allah wacce mijinta da babanta da ɗan'uwanta suka yi shahada a wannan yaƙin, a yayin da aka bata wannan labarin, buɗar bakinta sai ta ce, a wane hali Annabi (saw) yake, aka ce yana nan cikin ƙoshin lafiya, sai ta ce: ku nuna mini shi ko na samu nutsuwa, domin duk wata musiba da zata samu mutun in dai ta tsallake Annabi (saw) to ba komai ba ce, Allahu Akbar, bawan Allah ka duba ka ga yadda sahabbai suke tsananin son Annabi (saw) tabbas babu shakka duk Duniya ba wanda ya kama ko da farcen waɗannan bayin Allan wajen son Annabi (saw) duk wani

mai da'awar son Annabi (saw) yana bayan bayansu, Allah ya ƙara mana son Annabi (saw) zahiri da baɗini.

## Darussa

1- Haƙiƙa addinin Allah ba zai taɓa rabuwa da ƙulle ƙullen abokan gabarsa ba wajen ganin ƙarshensa, sai dai kuma Allah shi ya ke gudanar da kayan sa, a duk lokacin da wani ya yunƙuro don ganin ƙarshensa sai Allah ya ƙara ɗaukaka ambatonsa ya karya gadon bayan abokan gabarsa.
2- Maƙiyin ɓoye yafi na bayyane illa, domin shi na bayyane kana ganinsa ka san ta yadda za ka tunkareshi saɓanin na ɓoye, haƙiƙa Annabi (saw) ya kasance da maƙiyan ɓoye kuma sun cutar da shi ƙwarai da gaske, waɗannan maƙiya sune munafukai tawagar ɗan Salul.
3- burunƙasar Addinin Allah bai dogara da wani mutum ba, ko ka shigo a tafi tare da kai ko kuma ka tsaya a baɗe ka da ƙura kuma juyawarka da baya ba za ta rage Musulunci da komai ba, kamar yadda juyawarsu ɗan Salul ba ta rage musulmai da komai ba kuma ba ta sa sun yi ƙasa agwui'wa ba sun ja da baya.
4- Yana da kyau shugaba ya kasance ƙwararren jarumi masanin hanyoyin kawar da abokan gaba da masu laifi.
5- Haƙiƙa saɓa ma umarnin Annabi (saw) ba ya haifar da kyakkya-wan sakamako, bal, munmunan sakamako ya ke biyo bayan haka, domin wannan shine abun da ya kawo tasgaro a wannan yaƙin na Uhdu, ta yadda Annabi (saw) ya bawa maharba umarnin ka da su sakko daga kan wannan dutsen sawa'un musulmaine da nasara ko kuma akasin haka, da farko da suka bi wannan umarnin sai aka fara samun nasara, amma suna bijire masa sai labari ya

sauya, to wannan bai tsaya a iya rayuwar Annabi (saw) ba kaɗai, a duk lokacin da musulmai suka bijirewa bin umarnin Annabi (saw) to Allah zai ɗaura abokan gabarsu akansu ya cire musu kwarjini a idanunsu kamar yadda musulmai suke a yanzu.

6- Nasara da cimma gaci suna ƙarƙashin yiwa Annabi (saw) ɗa'a ta wajen bin karantarwarsa, rashin nasara kuma yana ƙarƙashin bijire masa.

7- Tsananin jarumtakar Annabi (saw) da Abubakar da Umar da Mus'ab da ma sauran sahabbai (ram)

8- Addinin Musulunci bai yarda da ƙasƙanciba ta yadda kowa zai faɗi abin da ya keso akansa kuma a kyale shi, a,a duk wanda ya faɗi mummunar Magana akansa to a mayar masa da martani ta hanyar ilimi.

9- ƙarfin imanin sahabbai da kuma tsananin soyayyarsu ga Annabi (saw)

10- Musulmi ba zai taɓa zama ba ba tare da wata jarabawaba, domin wannan rashin nasarar da musulmai suka fuskanta a wannan yaƙi jarabawa ce garesu, Allah ya yi hakanne don ya karrama wasun su da shahada, domin shahada kyautace daga Allah.

11- Sannan a wannan yaƙin mun fahimci cewa duk abin da zai iya samun sauran mutane na ciwo da raɗaɗi zai iya samun Annabi (saw), wannan ba tawaya ba ce a cikin haƙƙinsa, wasu annabawan ma mutanensu ne suke kashesu kamar yadda Allah ya ke bamu labari a cikin littafinsa mai tsarki.

**Yaƙin banun-Nadir**

Bayan yaƙin Uhudu kuma sai yaƙin banun-Nadir ɗaya daga cikin ƙabilun yahudawa guda uku mazauna Madina, haƙiƙa ya gabata ga-reka cewa Annabi (saw) ya kori ɗaya daga cikin ƙabilun nasu daga Madina, wato banu ƙai'nuƙa'a saboda makircinsu da yaudararsu, to wannan ma hakan take, wato ɗabi'arsu ta yaudara wacce suka shahara da ita suka ƙara nunawa, ta yadda suka ƙara tsananta ƙiyayyarsu ga Annabi (saw) da kuma makirce makircensu, har takai sun shirya hanyar da za su bi su kashe Annabi (saw) gaba ɗaya, wanda wannan shine dalilin korarsu da ga Madinar.

Da ga cikin yarjejeniyar da Annabi (saw) ya ƙulla da su, akwai taimako  atsakaninsu da shi ta wajen biyan Diya, ta yadda idan wani da ga cikinsu ya kashe wani can na daban to musulmai za su taimaka musu wajen biyan diyarsa, hakama su ma za su taimaka wa musulmai idan hakan ya faru garesu, to wani daga cikin sahabbai mai suna Amru ɗan Umayya ya kashe wasu mutane guda biyu bisa kuskure, sai 'Yan ƙabilarsu suka nemi Diya, sai Annabi (saw) ya je wajen waɗannan yahudawan na banun-nadir don su cika wannan yarjejeniyar, sai suka ce zamu aikata ya Baban ƙasimu ka ɗan zauna anan har mu biya maka buƙatarka sai ya zauna a jikin wata Katanga daga cikin katangun gidajensu, to sai Shai'ɗan ya kimsa musu kawai su kashe shi, sai suka sa wani daga cikinsu ya ɗauki dutsen markaɗe irin wanda ake ɗaurawa jaki igiya a haɗa shi da icen da ke jikinsa ya na juyawa da shi. domin su jefo ma Annabi (saw) akai, nan da nan sai Allah ya turo Jibrilu (as) da wahayi ya sanar da Annabi (saw) abin da suke shirin aikata masa, sai ya tashi da sauri ya tunkari Madina ya labarta ma sahabbansa abin da yahudawan banun-Nadir suka yi shirin aikata masa.

Annabi (saw) ya aika musu da saƙon cewa su yi maza maza su haɗa komatsansu su bar Madina ba a buƙatar sake ganinsu, har sun fara haɗa kayansu sai ɗan Salul shugaban munafukai ya aika musu cewa ka da su je ko'ina, su yi zamansu, ya tabbatar musu da cewa zai taimakesu, sai wannan ya ruɗesu suka ƙi fita, Annabi (saw) ya tsaresu a cikin ganuwarsu ya sa aka sassare Dabinansu aka babbanka musu wuta.

A yayin da suka ga uwabbari kuma suka ji ɗan Salul da ya yi musu alƙawarin taimako shiru kamar an shuka dusa, sai suka aikawa Annabi (saw) cewa zasu fita da matayensu daƳaƳansu da kuma kayan raƙumi guda amma ban da makaman yaƙi, Annabi (saw) ya basu damar hakan.

Dukiyarsu ta zama mallakin Annabi (saw) shi kaɗai sai abun da ya gadama zai yi da ita, ya kasance ya na sa ta a cikin maslahar musulmai, domin (fai'i) ce, wannan shine sakamakon makirai mayaudara.

**Darussa.**

1- Har abada bayahude ba zai taɓa sararawa musulmi ba, domin ƙiyayyarsa gareshi a jini take.
2- bayyanar Alama mai ƙara gasgata manzancin Annabi (saw) ta yadda Allah ya aiko masa da Jibrilu don ya sanar da shi makircin da abokan gabarsa suke ƙulla masa.
3- Halaccin salwantar da dukiya domin tabbatar da wata maslaha marinjayiya.
4- ƙarshen mayaudari taɓewa da halaka.

5- zafafawa da tsanantawa suna da nasu anfanin, domin akwai wajen da idan babu su to lamura za su dagule ba za a samu cimma gaci ba.

## Yaƙin Ahzab (Kandaƙ)

A yayin da abokan gabar Addinin Allah suka ga yadda Musulunci ya samu tamkini a bayan ƙasa aka kwashe shekara guda ba a sake wani yaƙi ba tsakanin musulmai da mushirikai, domin sun jaraba ba su ji da daɗi ba suka gane cewa lallai musulmai ba kanwar lasa bane, to idan baka mantaba a baya ka ji irin korar Karen da Annabi (saw) ya yiwa yahudawa sakamakon yaudararsu da gogewarsu wajen iya ƙulla makirci da tuggu.

Duk da kasancewar abin da ya sami yahudawan nan ba su ɗau izina ba sun shiga taitayinsu, bal, a yayin da suka ga irin cigaban da addinin Allah ya samu da irin yadda daular Musulunci take ta burunƙasa ta na ƙara kafuwa, sai wutar baƙin ciki da hassada da adawa ta ƙara ruruwa a zukatansu, dan da nan suka haɗa gangami suka garzaya wajen ƙurai'shawa suna masu kwaɗaitar da su akan su haɗa wata bataliyar runduna su gayyaci duk wanda zasu iya gayyata kuma su ma su na ciki, domin a haɗu a yiwa musulmai taron dangi a musu ruddugu a murƙushesu gaba ɗaya, sai ƙurai'shawa suka yi na'am da wannan tunanin, suka shiga haɗa kan sauran 'Yan'uwansu mushirikai domin iyar da wannan kudirin nasu, suka tara sojojin yaƙi waɗanda adadinsu ya kai dubu goma (10,000) wanda mutanen Madina mazansu da matansu yaransu da manyansu ba lallai ba ne su kai wannan adadin, suka durfafo Madina don aiwatar da kudirinsu.

A yayin da labari ya riski Annabi (saw) sai ya nemi shawarar sahabbansa akan yaya za a ɓulloma lamarin, sai Suhaib Arrumi ya ce: mu a ƙasarmu ta Faris idan aka mana zobe to muna haƙa babban rami ne mu zagaye garin gaba ɗaya da shi mubar ƙasar ta ciki a samu waɗanda suka kware a wajen iya harbi da kwari da baka a zuba su a kowace fuska daga cikin fuskokin garin ta yadda da wani ya yi gigin tsallakowa sai su mayar da shi ta hanyar yi masa ruwan kibbau, Annabi (saw) ya yi na'am da wannan shawarar ya sa aka gina rami wanda tsawonsa ya kai zira'i dubu biyar faɗi kuma zira'i tara zurfi kuma zira'i goma sha bakwai,

Kuma shima Annabi ya yi tarayya da sahabbai ta wajen ginasa, wanda an gina wannan raminne alokacin tsananin sanyi da yunwa da ƙarancin abun hannu, ana cikin gini sai aka zo kan wani falalen dutse gagara fasuwa, sahabbai suka yi su fasa shi amma abu ya ci tura, sai suka gayawa Annabi (saw) halin da ake ciki, sai ya zo ya amshi Diga ya ambaci sunan Allah ya bugi dutsen sai ɗaya bisa ukun sa ya dagargaje, Annabi (saw) ya ce: Allah mai girma an bani mabuɗan Sham a yanzu hakama ina ganin fadar sarautarta, ya kuma bugun dutsen ya kuma rugujewa ya yi kabbara ya ce: an bani mabuɗan Faris, ya kuma saransa ya ƙara rugujewa ya ce: an bani mabuɗan Yamen a yanzu hakama ina ganin ƙofofin San'a'a a wannan lokacinne dutsen ya baje gaba ɗaya.

Wannan yaƙin ya farune a watan shawwal a shekara ta biyar bayan hijira.

A wannan yaƙinne wata mu'ujiza ta Annabi (saw) mai ban sha'awa ta bayyana, idan ba ka mantaba ka ji cewa an yi wannan yaƙin a

cikin tsananin yunwa da ƙarancin abun hannu, to Jabir ɗan Abdul-lahi ya ga cikin Annabi (saw) ya ɗamfare don yunwa, sai ya je gida ya yanka wani ɗan taure ya sa matarsa ta niƙa sa'i ɗaya na alkama ta sana'anta musu gurasa, sai ya nema daga Annabi (saw) akan ya zo tare da wasu 'Yan tsiraru da ga cikin sahabbansa mutun ɗaya zuwa biyu domin su ci wannan abincin da ya tanada dominsa, sai Annabi (saw) ya kwashi dukkan sahabban da suka halarci Kandaƙ ya taho da su, wanda sun kai su dubu (1000) ya ce: kasanar da matarka ka da ta sauke tukunyar daga kan wuta, Jabir ya koma ya sanar da matar abin da Annabi (saw) ya ce, kana ya ce da ita kaiconki ga Annabi nan da dukkan sahabbai, sai ta ce: shin ya tambayeka game da hakan? Ya ce: eh, sai ta ce ka da ka damu ba za mu ji kunya ba, sai da sahabban da suka halarci wannan yaƙin na Kandaƙ suka ci abincin nan suka ƙoshi, wannan ba ƙaramin dalili bane mai ƙara tabbatar da manzancin Annabi (saw)

Haƙiƙa munafukai sun firgita kuma sun razana ƙwarai da gaske a wannan yaƙin, suka yi wujiga wujiga dasu suna ta faɗar maganganu suna cewa daman alƙawarin da Allah da mazansa suka yi mu su ba gaskiya bane, kawai yaudarane.

Su kuma makirai iyayen makirci waɗanda ko Sheɗan ya basu lambar girmamawa da jinjina wajen iya makirci da ƙulle ƙulle, wato yahudawa, yayin da suka ga musulmai sun shagalta da fuskantar rundunar abokan gaba sai suka ƙara ƙaimi da hazaƙa wajen inganta sana'arsu ta makirci da ƙulle ƙulle, daman waɗanda suka rage daga cikin ƙabilunsu guda uku sune banu ƙurai'za, ana cikin haka ne sai shugaban yahudawan banun-Nadir wanda shine kanwa uwaggami na assasa wannan yaƙin ya laɓaɓa ya shiga unguwar banu ƙurai'za

ya kwaɗaitar da su akan warware alƙawarin dake tsakaninsu da Annabi (saw) akan su bada haɗin kai wajen yaƙarsa, da farko sai shugabansu ka'abu ɗan Asad Alƙurazi ya cije ya ce ba zai warware alƙawarin dake tsakaninsu da Annabi (saw) ba, amma sai wannan fajirin malalacin bayahuden Huyayyu ɗan Akɗab ya nace masa har ya yarda, yayin da labari ya riski Annabi (saw) sai ya tura Sa'adu ɗan Mu'azu da Sa'adu ɗan Ubada shuwagabannin ƙabilun Aus, da Kazaraza don su tabbatar da gaskiyar zancen, suka dawo suka tabbatar masa da lallai haka al'amarin yake, musulmai suka ƙara shiga cikin wani tashin hankali ya zama gaba kura baya Siyaki.

Da ƙunci ya kai ƙunci sai Annabi (saw) yai nufin ya yi sulhu da abokan gaba a bisa cewa duk abin da aka samu na anfanin ƳaƳan itatuwa za a basu ɗaya bisa uku, ya nemi shawarar Sa'adu ɗan Mu'azu da Sa'adu ɗan Ubada meye mahangarsu akan haka, suka ce idan Allah ne ya umarceka da hakan to mun bi kuma mun yarda, idan kuma wannan daga garekane to ba mu da buƙatar haka, domin lokacin da mu ke kan shirka muke addini ɗaya dasu, ba su taɓa kwaɗayin cin amfanin itatuwanmu ba sai dai idan mun yi musu garar baƙi ko kuma su siya da kuɗinsu, to tayaya kuma yanzu zamu yarda da wannan ƙasƙancin bayan Allah ya ɗaukakamu da Musulunci da kuma kai, sai Manzan Allah (saw) ya karɓi wannan tunanin nasu.

To cikin ni'imar Allah ga musulmai sai ya yi amfani da wani mutun guda ɗaya wajen kashe wutar makircin abokan gabar cikin gida wato banu ƙurai'za, wannan mutumin shine Nu'aimu ɗan Mas'ud, ya kasance ya na daga cikin Ƴan ɓangaren banu ƙurai'za a jahiliyya, to ashe ya musulunta ba tare da kowa ya sani ba, sai ya sanar da

Annabi (saw) musuluntarsa, ya tanbaye shi ko zai umarceshi da wani abu a wannan yaƙin, sai Annabi (saw) ya ce masa ka je ka yi abin da zaka iya yi wajen rusa kai'din abokan gaba ta hanyar nuna musu ba ka tare da mu, domin shi yaƙi ɗan zamba ne, sai ya garzaya wajen banu ƙurai'za ya ce musu: kun san dai ni mai matuƙar ƙaunarku ne, suka ce gaskiyane, sai ya ce: lallai ku kun yaƙi Muhammadu, kuma ƙurai'shawa da Gaɗafanawa idan suka samu nasara akan sa shikenan abun nema ya samu, idan kuma ba su samu ba sai su koma garuruwansu, ku kuma ba kamarsu kuke ba, wannan garinku ne kuma da matanku da Ƴaƴanku duk suna ciki, idan ƙurai'shawa ba su samu nasaraba suka koma gidajensu, to ku kuma Muhammadu zai ɗau mataki akan ku, kamar yadda ya ɗauka akan Ƴan'uwanku, saboda haka ka da ku yi yaƙi da su har sai sun ba ku jingina, sai suka ce: haƙiƙa ka zo da tunani mai kyau.

Daga nan sai ya tafi wajen ƙurai'shawa ya ce da su: haƙiƙa kun san irin ƙaunar da nake nuna muku da kuma nasiha ta a gareku, sai suka ce gaskiyane, sai ya ce to haƙiƙa yahudawa sun yi danasani akan warware alƙawarin dake tsakaninsu da Annabi (saw) a yanzu hakama sun goyi bayan Annabi (saw) kuma sun aika masa da saƙo cewa za su yi dabara su karɓi jinginar makamanku su ba shi dan ya yaƙe ku, sannan su taimake shi akan ku, sai suka ce yanzu meye abun yi? Sai ya ce: idan suka tambayeku jingina kar ku ba su, sannan sai ya tafi wajen Gaɗafanawa ya gaya musu kwatan kwacin abun da ya gaya wa ƙurai'shawa.

Da ranar asabar ta zagayo sai ƙurai'shawa da Gadɗafanawa suka aikawa yahudawa suna ma su cewa: mu ba mazauna wannan ƙasar ba ne, kuma dabbobin da mu ke hawa sun halaka. Saboda haka ku

hanzarta zuwa garemu domin mu gaggauta kawar da Muhammadu, sai yahudawa suka aika mu su cewa mu ba za muyi yaƙi tare da ku ba har sai kun bamu jinginar makamanku, yayin da wannan saƙon ya riski ƙuraish da Gaɗafan sai suka ce: haƙiƙa Nu'aimu ɗan Mas,ud ya yi gaskiya, sai suka sake aika musu cewa wallahi ba za mu baku jinginar komai ba saboda haka ku fito mu gaggauta kawar da Muhammadu, sai suma yahudawa suka ce: wallahi Nu'aimu ya yi gaskiya, sai kowane ɓangare ya yi baran baran da ɗayan ɓangaren Allah jalla wa'alah ya wargaza kai'din su ya isar ma musulmai da ga makircinsu ta hanyar wannan ɓoyayyan musulmin Nu'aimu ɗan Mas'ud (ra)

Annabi (saw) kuma na can yana ta roƙon Allah yana cewa: ya Allah kaine mai saukar da littafi, mai saurin hisabi, ka tarwatsa taron waɗannan abokan gabar addinin ka waɗanda suke neman murƙushe shi, ya Allah ka tarwatsa suka sanya musu girgizar ƙasa.

Allah maji roƙo ya amsa addu'ar Annabinsa (saw) ya aiko musu da rundinarsa gagara yin fito na fito da ita, wannan rudunar ita ce iska da guguwa mai ƙarfi, ta zo ta dinga tunɓuke tantinansu da hemominsu ta na tsits'tsinka igiyoyin da aka ɗaɗɗaure tantinan da su, ba ta bar musu wata tukunya ba wacce suke girke girke da ita face ta kifar da ita, daga nan Allah ya tarwatsa wannan rundunar ya ɗaiɗaita taronsu suka tarwatse kowa ya cikawa rigarsa iska ya ƙara gaba, wanda Allah da kan shi ya ɗau ragamar yaƙin ya hutar da musulmai, da haka yaƙi ya kawo ƙarshe.

**Darussa:**

1- Kamar yadda ake ta maimaitawa, abokan gabar Addinin Allah ba zasu taɓa gushewa ba suna masu kwaɗayin samun wata kafa da za su bi ta cikin ta su cutar da musulmai, saboda haka ya na da kyau musulmai su zama cikin takatsantsan da su, domin duk irin soyayyar da za su nuna maka a zahiri ba zata hana su cutar da kai ba a matsayin ka na musulmi, domin ba ta kai zuci ba.
2- Kafurci tafarki ɗayane, duk inda wani kafuri ya ke burinsa bai wuce ya ga ƙarshen musulmai ba, koda kuwa a kwai banbancin aƙida atsakaninsu isu isu, abin da ya ke faruwa a Isra'ila ahalin yanzu ya isa shai'da akan haka, kowa ya ga yadda suke ta kashe musulmai amma babu wata ƙasa daga cikin ƙasashen kafurai masu rajin kare haƙƙin ɗan Adam da suka tsawatar musu ko kuma suka nuna damuwarsu akan abin da suke aikatawa, bal, su suke ƙara ƙarfafa musu gwuiwa ta hanyar basu makamai na ƙare dangi!
3- irin halin da Annabi (saw) da sahabbai suka tsinci kansu a ciki na ƙarancin abun hannu.
4- Halaccin yin ƙarya a wajen yaƙi don rikita abokan gaba ta hanyar shigo musu da abin da zai raba kansu, kamar yadda wannan sahabi ya yi, domin shi yaƙi ɗan zambane.
5- A duk lokacin da musulmai suka tsayu akan gaskiya da ɗa'a ga Allah da manzansa (saw) to Allah ba zai taɓa ɗaura abokan gabarsu ba akansu, ko a yau musulmai suka koma zuwa ga Allah jalla wa'ala to wannan alƙawari na nasara da samun galaba da ɗaukaka akan abokan gaba yana nan, ba zai taɓa gushewa ba,

idan musulmai suka ga akasin haka to su tanbayi kawunansu lai’fin daga gare sune.

## Yaƙin banu ƙurai’za

Idan ba ka mantaba a baya ka ji yadda yahudawan banu ƙurai’za suka warware alƙawarin dake tsakaninsu da Annabi (saw) to bayan an gama yaƙin Ahazab an samu nutsuwa, watarana Annabi (saw) ya na gidan Ummu Salma (ra) ya na wanka, sai mala’ika Jibrilu (ra) ya zo masa ya ce da shi: shin har ka ajiye makamin yaƙine, haƙiƙa mala’iku ba su ajiye nasu makaman ba, ka fita zuwa ga banu ƙurai’za, sai Annabi (saw) ya sanar da sahabbai suka yi gangami suka tunkari unguwar banu ƙurai’za, ya ba Aliyu (ra) tuta, ya ba Abdullahi ɗan ummu Maktum jiran gari, Annabi (saw) ya fita tare da rundunarsa kimanin mutun dubu uku (3,000) ya tsaresu tsawon kwana ashirin da biyar, yayin da ƙunci ya kai ƙunci a garesu sai shugabansu ya bijiro musu da abubuwa guda uku: ko dai su musulunta, ko kuma su kashe ƳaƳayensu da matayensu da hannayensu sannan su fito da takobbansu tsirara su yi taho mu gama da Annabi (saw) su gaggauta masa, ko kuma su bari sai ranar Asabar su afka ma sa, domin su na da yaƙinin samun nasarar yaƙi a wannar ranar, amma ba su karɓi ɗaya daga wannan tayin nasa ba, daga ƙarshe dai sai suka mika wuya zuwa ga Annabi (saw) a kan hukuncin da ya tanadar musu ya aika musu da Abu Lubaba a yayin da suka nemi hakan don su yi shawara da shi akan wannan lamari, domin dukiyarsa tana yankinsu, sai suka ce masa: kana ganin mu mika wuya zuwa ga hukuncin Annabi (saw) ya ce: eh, yai musu ishara zuwa ga wuyansa, alamar cewa hukuncin shine za a yankasu, sai

kuma ya yi nadama ya tuna cewa ya ha'inci Allah da manzansa, sai ya je ya ɗaure kansa a filar Masallaci har Allah ya saukar da aya akansa ya yi masa afuwa.

Annabi (saw) ya turo musu Sa'adu ɗan Mu'azu don ya faɗi hukuncin da ya dace da su, su suna ganin sauƙi ya zo tunda akwai alaƙa a tsakaninsu kafun zuwan Musulunci, amma sai ya ce musu ba sani ba sabo, ya ce kawai a kashe duk wani baligi daga mazajensu a maida matansu bayi dukiyarsu kuma ta zama ganima ga musulmai, Annabi (saw) ya sa aka haƙa rami a kasuwar madina aka sassare musu kai, tun daga wannan lokacin sai aka zauna lafiya aka yada ƙwallon mangwaro aka huta da ƙuda.

**Darussa:**

1- Halaccin kawar da duk wani wanda ya ke zama barazana ga rayuwar al'umma da ma ƙasa baki ɗaya, duk wani wanda ya ke kawo rashin kwanciyar hankali a cikin rayuwar al'umma kuma ya ke zama barazana garesu to ya halatta ga hukuma ta ɗau mataki mai tsauri akansa koda ta hanyar kawar da shi ne a bayan ƙasa gaba ɗaya, domin rai bai'fi rai ba, wannan abu da Annabi ya sa aka yi shine madarar adalci da kawo daidaito a cikin al'umma, hatta abokan gabar Musulunci muna ganin yadda suke ɗaukan matakin kisa akan wanda ya ci amanar ƙasa, to babu cin amanar da ta kai ta waɗannan yahudawan, domin sun tara makamai na ƙare dangi da niyar shafe musulmai gaba ɗaya, sai Allah ya wargaza makircinsu ƙaiƙayi ya koma kan masheƙiya.
2- Babu wani wanda zai iya kuɓuta daga aikata zunubi duk yadda ya kai da tsoron Allah in ka ɗauke Annabawa a bisa zance mafi

inganci, sai dai abin da aka fi so ga mai lai'fi shine tuba da nadama.

## Yaƙin banu Musɗaliƙ

Bayan tunɓuke waɗannan miyagun yahudawan sai aka samu zaman lafiya da kwanciyar hankali daular Musulunci ta ƙara kafuwa mutane suka yi ta shiga addinin Allah, ana nan a haka sai labari ya riski Annabi (saw) cewa ƙabilar banu Mustaliƙ ƙarƙashin jagorancin shugabansu Haris ɗan Darar su na shirya mayaƙa dan yaƙarsa, sai Annabi (saw) ya aika musu Burai'da ɗan Husai'b a matsayin ɗan leƙen asiri domin ya binciko gaskiyar labarin, sai ya dawo ya tabbatarma da Annabi (saw) ingancin labarin, sai Annabi (saw) ya tara mayaƙansa ya tunkaresu, sai musulmai suka haɗu da ɗan leƙen asirin abokan gaba suka kama shi suka kasheshi, yayin da labarin isowar Annabi (saw) da tawagarsa ya isar ma banu Mustaliƙ, sai suka razana matuƙa, a yayin da Annabi (saw) ya isa inda suke sai ya kai mu su hari, bayan ya yi galaba a kansu sai ya kama matansu da ƳaƳansu da dukiyoyinsu na daga dabbobi ya kashe na kashewa masu gudu suka gudu, daga cikin ribatattun yaƙin akwai Juwairiya uwam muminai Ƴar sarkin na su, sai Annabi (saw) ya Ƴantata ya aureta, to ganin haka sai sahabbai su ma suka Ƴanta sauran ribatattun da ke hannunsu waɗanda sun kai Ƴan gida ɗari, suka ce tayaya zamu bautar da sirikan Annabi (saw) wanda hakan ya sa suka musulunta gaba ɗaya.

A cikin wannan yaƙinne Annabi (saw) ya fita tare da wata tawaga ta munafukai, waɗanda sun cutar da shi ƙwarai da gaske, kuma sun bayyana abin da yake ɓoye a zukatansu na ƙin musulmai da tsanarsu har takai ga cewa sun taɓa mutuncin Annabi (saw) ta

yadda suka jefi matarsaƳar lelensa da lai'fin zina! Ga ƙissar nan daki daki:

## ƙiran ƙarya ga sayyada A'isha Assiddiƙa

Annabi (saw) ya kasance idan zai yi balaguro (tafiya) to ya kan yiwa matansa ƙuri'a, duk wacce ƙuri'a ta faɗa kan ta to da ita za ayi wannan balaguron, to a wannan yaƙinma hakan ta kasance ta yadda ƙuri'a ta faɗa kan A'isha, sai Annabi (saw) ya fita tare da ita, wanda hakan ya farune bayan saukar ayar hijabi, akan hanyar dawowarsu ne suka yada zango, sai A'isha (ra) ta zagaya dan biyan buƙatarta, sai ta shafa ƙirjinta ba ta ji sarƙatta ba, sai ta koma dan nemanta wanda hakan ya sa ta jinkiri har Annabi (saw) ya ba da umarnin tafiya, sai waɗanda suke ɗaukan Hau'daj ɗinta (ɗaki ɗan ƙarami dai'dai mutun ɗaya wanda ake ɗauka akan doki) suka zo suka ɗauka azatonsu ta na ciki, domin ƙarancin girman jikinta da kuma nauyinta, rundunar ta ɗaga ta ci gaba da tafiya, a daidai wannan lokacinne kuma A'isha (ra) ta iso masaukin na su bayan ta yi nasarar ganin Sarƙar tata, ta na zuwa sai ta taradda wajan wayam ba ko mutun guda daga cikin ayarin nasu, sai ta samu waje ta zauna tana tsammanin za su dawo nemanta, ta na nan a haka sai bacci ya ɗauketa, to akwai wani sahabi mai suna Safwan ɗan Mu'aɗɗal, ya kasance a bayan rundunar ya ɗan taɓa bacci, sai ya tashi a ƙarshen dare dan ya cim masu, sai kawai ya ga mutun kusa da shi sai ya yi istirja'i (faɗar: Inna lillahi…) to ya na ganinta sai ya ganeta kawai sai ya gurfanar da dabbarsa ta hawa bai ce ma ta ta kanzil ba ita ma ba ta ce masa ko (eh) ba, sai ta lulluɓe fuskarta da mayafinta ta hau kan dabbar suka tafi shi ya na gaba ya na jan abar hawan har suka tadda rundunar bayan sun yada zango a ƙarshen dare don hutawa.

To daga nanne fa kasuwar baje kolin munafukai ta soma ci ƙarƙashin jagorancin shugaban majalissar munafunci ta ƙoli, wato ɗan Salul Allah ya baƙanta fuskarsa, kawai sai ya ƙirƙiri wani sharri na jifan waɗannan bayin Allah guda biyu da zina, wanda abin da hakan yake nufi suka ga Annabi (saw) ta hanyar ɓata shimfiɗarsa.

Labari ya watsu a Madina al'amura suka rincaɓe mutane suka dinga yamiɗiɗi da wannan Magana ba tare da bibiyar ingancinta ba, Annabi (saw) ya canza ma nana A'isha gaba ɗaya, iyakacinsa da ita kawai sai dai ya ɗan daga labule ya ɗan leƙo ya tambayi lafiyarta ya koma, ita kuma bai'war Allah ba ta san wainar da ake toyawa ba, sai watarana ta ɗan zagaya tare da ummu Misɗahu don biyan buƙata sai ummu Misɗahu ta yi tuntuɓe mayafin ta zai taɗiyeta ya kada ita, sai ta ce Misɗahu ya halaka! Sai A'isha ta ce da ita tir da abin da ki ke faɗa, shin ki na zagin mutumin da ya halarci yaƙin Badar, sai ta ce da A'isha: ya wacce ba ta san makirce makircen mutane ba, shin ba ki san abin da ya ke faɗa bane akan ki, sai ta ce: me ya ke faɗa a kai na? Sai ta labarta ma ta abin da ya ke wakana, daman ba cikakkiyar lafiya ta ke da ita ba sai rashin lafiyarta ya ƙaru.

A yayin da nana A'isha Ta koma gida sai Annabi (saw) ya leƙo kamar yadda ya saba, sai ta ce da shi: ka yi mini izini in je wajen iyayena, ta yi hakane don ta samu tabbacin ingancin labarin a wajensu, sai Annabi (saw) ya yi ma ta izini.

Annabi (saw) ya nemi shawarar wasu daga cikin sahabbansa akan wannan rikitaccen al'amarin, kowa sai alkairi da son barka ya ke faɗa akan ta musammam ma waɗanda suke zama tare da ita.

Ana nan a haka ana jiran hukuncin Allah daga sama, sai Allah cikin hikimarsa ya saukar da ayoyi waɗanda suke wanke A'isha daga wannan ƙazafin da aka yi ma ta, Allah ya kunyata munafukai maƙaryata masu neman duk wani mumini da sharri, su kuma musulman da sheɗan ya yi galaba akan su suka gasgata munafukai har ma suka ja ragamar yaɗawa da watsawa ba tare da bin diddigin labarin ba domin tabbatar da gaskiyarsa, Annabi (saw) ya sa aka yi musu bulala ɗari ɗari (100) sakamakon ƙazafi.

**Darussa:**

1- Abokan gabar addinin Allah ba za su taɓa gushewa ba su na neman hanyar da za su bi su murƙushe shi gaba ɗaya.
2- Ka fara ɗaukan mataki akan maƙiyin ka kafun ya ɗau nasa matakin da ya ke shirin ɗauka akan ka.
3- Haƙiƙa kyautatawa ta na ɗaya daga cikin manyan jigogin da suke bada gudummuwa ta wajen jawo hankalin wanda ya ke gaba da addinin Musulunci zuwa ga ƙaunarsa da kuma karɓarsa.
4- Girmama dangin matar wani shugaba ga mabiyansa yana da kyau ƙwarai da gaske, ta yadda sahabbai suka saki dangin Juwairiyya dan girmama Annabi (saw)
5- Yadda sahabbai suke matuƙar girmama Annabi (saw) wanda har hakan ya bayu zuwa ga girmama duk wani wanda ya ke da alaƙa da wanda ya raɓeshi.
6- A da ana ganin an samu lafiya tun da aka kawo ƙarshen yahudawan Madina, to ashe akwai wata sabuwa, wato bayyanar munafukai, wanda makircinsu ya ƙara fitowa fili bayan tunɓuke yahudawa suka dinga fito da salo daban daban na cutar da musulmai, wanda tasirin sharrin waɗannan mutanen ma yafi na

yahudawa a cikin musulmai, domin su abokan gabane na ɓoye, ma'anar (munafuki) a shara'a: shine wanda ya ke bayyana Musulunci da ƙauna ga musulmai a zahiri, ya ke ɓoye kafurci a baɗini, wanda a Madina aka fara samunsu, kasancewar daular Musulunci ita ta ke da faɗa a ji saɓanin Makka.

7- Musulmi a koda yaushe baya rabuwa da jarabawa daga Allah, wanda hakan darajace mai girma a wajansa shi kuma bai sani ba.

8- idan kafuri ya rasa hanyar da zai bi ya cutar da musulmi ta zahiri, to sai ya koma yana neman abin da zai ɓata masa mutunci da shi.

9- Ba ya dacewa ga musulmi ya kasance cewa ba ya kyautata wa ɗan'uwansa zato ta yadda da ya ji wani yamiɗiɗi a kansa sai shima ya ɗauka ya cigaba da yaɗawa batare da bincike ba kamar yadda ya faru ga wasu musulman da suka halarci wannan yaƙin, a a musulmi ya kasance mai nemawa ɗan'uwansa uzuri da yi masa kyakkyawan zato a koda yaushe.

10- Hukuncin ƙazafi a Musulunci bulala ɗari ne (100)

11- Falalar sayyada A'isha ta yadda Allah ya wanketa daga saman bakwai.

12- Wannan ƙissar tana ƙara tabbatar mana da cewa Annabi (saw) bai san gai'bu ba, domin da ya san gai'bu da ya gane cewa ƙazafi aka yiwa A'isha, da bai tsaya jiran saukar wahayi ba, wannan shine ingantaccen zance wanda zahirin dalilai na shara'a suke ƙarfafa, kuma wannan ba tawaya ba ce ga Annabi (saw) bal, yana da mu'ujizozin da suka fi ma sanin gai'bu ban al'ajabi.

Haƙiƙa wannan ƙissa tana da fa'idoji da darussa masu yawa wanda ba zai yiwu mu kawosu duka ba saboda gudun tsawaitawa.

## Yaƙin Hudai’biyya

Bayan faruwar waɗannan abubuwa da ambatonsu ya gabata nasara ta fara tabbata ga musulmai a kan abokan gabarsu, sai Annabi (saw) ya yi azamar zuwa Makka dan aikin umara, wanda dama an nuna masa a mafarkinsa gashi ya shiga masallaci mai alfarma har ma ya karɓi makullan Ka’aba kuma gasu nan sun yi ɗawafi da umara har sun yi hilli (sun ƙare aikin umara) sai ya ba sahabbansa labarin wannan mafarki suka yi farin ciki da shi, wannan ya farune a shekara ta shida ta annabci.

Annabi (saw) ya fita tare da sahabbai kimanin dubu ɗaya da ɗari huɗu (1,400)

A yayin da ya iso Zul’hulai’fa (miƙati ne na mutanen Madina) sai ya ɗaura harami da umara ya yiwa hadayarsa taƙalidi (ma’ana ya rataya mata takalmi ko wani ɗan kyalle dan banbanceta da wacce ba hadaya ba, hadaya sune raƙuma ko shanu da mahajjaci yake kai su ɗakin Ka’aba dan a yanka a ciyar da mabuƙata daga namansu don neman kusanci da lada a wajen Allah) sannan ya yi ish’arin su (ish’ari: shine a tsaga musu gefen tozonsu na dama har jini ya fito) sai ya aika ɗan leƙen asiri daga ƙabilar Kuza’a don ya binciko masa labarin ƙurai’shawa, Annabi (saw) da sahabbai suka cigaba da tafiya har suka kai wani waje da ake kira da Usfana, sai ga ɗan leƙen asirin ya dawo yana mai cewa ƙurai’shawa sun tara maka mayaƙa dan su hanaka shiga Makka, sai Annabi (saw) ya nemi shawarar sahabbai, ya ce: kuna ganin mu tasamma mataye da ʽYaʽYayen waɗannan da suke neman hanamu zuwa ɗakin Allah, sai Abubakar (ra) ya ce: mu dai mun zo ne don yin umara ba don yaƙi ba, kawai abin da ya dace

muyi kawai mu tunkari garin duk wanda ya yi ƙoƙarin hanamu shiga sai mu yaƙeshi, Annabi (saw) ya karɓi wannan shawarar ya bada umarni da a cigaba da tafiya.

Su kuma ƙurai'shawa dama suna samun labarin fitowar Annabi (saw) sai suka shiga mitin ɗin gaggawa suka yanke shawarar hanashi shigowa Makka, suka turo rundunar mayaƙa kimanin ɗari biyu (200) ƙarƙashin jagorancin Kalid ɗan Walid, suka kafa sansani a wani waje da ake kira Usfana dake kan babbar hanyar Makka, Annabi (saw) ya yi salatul kaufi sannan ya canza hanya don kaucewa yaƙi da Kalid bini Walid, domin shi ba abin da ya kawoshi ba kenan, yayin da Kalid ya ga haka sai ya gaggauta komawa zuwa Makka dan ya sanar da ƙurai'shawa halin da ake ciki, sai suka fito suka kafa sansani a wajen da ake kira da Baldah, wani kwazazzabone kusa da Tan'im, shi kuma Annabi (saw) ya ci gaba har ya kai gab da Hudai'biyya sai taguwarsa ƙaswa'a ta gurfana a ƙasa, sai sahabbai suka ce: ƙaswa'a ta cije ta tsaya, Annabi (saw) ya ce: ba cijewa ta yi ba, wannan ba halinta ba ne kawai dai wanda ya hana giwa tunkarar Ka'aba dan ruguzata shi ya tsareta, daga nan sai ya zabureta sai ta miƙe ta ci gaba da tafiya har suka kai Hudai'biyya (Hudai'biyya: sunan rijiyane da ke wannan wurin).

Daga nan Annabi (saw) ya tura 'Yan saƙo domin su sanar da ƙurai'shawa cewa ba yaƙi suka zo yi ba kawai sun zo aikin umarane, suma ƙurai'shawa suka yi ta turo manzanninsu suna tattaunawa da Annabi (saw) har aka cimma yarjejeniya akan cewa Annabi (saw) ba zai shigo Makka ba a wannan shekarar sai shekara mai zuwa, sannan za a tsagaita wutar yaƙi a tsakanin ɓangarorin guda biyu na tsawon shekara goma, sannan kuma duk wanda yake so ya marawa

Annabi (saw) baya ko ya marawa ƙurai'shawa baya a wannan yar-jejeniyar to yana da damar hakan, sannan kuma duk wanda ya bar Makka ya je Madina wajen Annabi (saw) dan karɓar addininsa to za a dawo da shi, wanda kuma ya bar Madina ya yi ridda ya koma Makka to ba za a dawo da shiba.

Sai Annabi (saw) ya kira Aliyu don ya rubuta wannan yarjejeniyar, sai Annabi (saw) ya fara mai shifta da (bismillahir rahmanir Rahim) Sai wakilin ƙurai'shawa Suhai'lu ya ce: shi bai san wannan ba sai an goge, haka ma da aka rubuta: wannan shine abun da muhammadu manzan Allah (saw) ya yi sulhu da shi. sai ya ce sai an goge (rasulullah) domin inda sun yarda shi manzan Allahne da basu yaƙe shiba, Annabi (saw) ya umarci Aliyu (ra) da ya goge, sai ya ce: shi ba zai iya goge wannan sunanba da hannunsa, Annabi (saw) ya goge da kansa.

Haƙiƙa Umar ya nuna tsananin fushinsa akan wannan hukuncin na zalunci, amma Annabi (saw) ya nuna masa komai mai wucewa ne.

Ana cikin rubuta wannan sulhu mai ƙunshe da rashin adalci sai ga Abu Jandal ɗaya daga cikin musulman da ke Makka waɗanda aka hana su yin hijira ya samu ya tsallako wajen musulmai, sai Annabi (saw) ya sa aka mayar da shi bisa kafewar Suhai'lu a kan hakan, Annabi (saw) ya ce ya yi haƙuri Allah zai kawo masa mafita da shi da ire - irensa.

Bayan an koma Madina, sai ɗaya daga cikin musulman da ƙurai'shawa suka hana hijira wanda ake kira da Abu Basir ya samu ya gudo Madina, Annabi (saw) ya sa aka mayar da shi bisa yarjejeniyar da ke tsakaninsa da ƙurai'shawa bayan sun aiko mutum biyu

daga cikinsu akan buƙatar dawo da shi, suka tafi da shi har suka kai Zul'hulai'fa, sai suka yada zango suka fara cin abinci, sai Abu Basir ya ce da ɗaya daga cikinsu: kai wannan takobin taka tana da kyau, sai ya ce: gaskiyane tabbas tana da kyau, sai Abu Basir ya ce: ɗan ban mugani, sai ya ba shi, sai Abu Basir ya zabura ya ɗauke masa kai, sai ɗayan ya gudu ya koma Madina har ya shiga masallaci, daga nan kuma duk wanda ya gudo sai ya haɗe da Abu Basir, daga nan suka zama barazana ga fataken ƙurai'shawa, da kansu suka nemi a janye wannan yarjejeniyar ta zalunci.

**Darussa:**

1- Shar'anta aikin umara da kuma falalarsa a Musulunci ta yadda Annabi (saw) ya ɗebi ɗaruruwan sahabbansa a lokacin hatsari da tsoro don gabatar da wannan ibadar.
2- Abokan gabar addini ba zasu taɓa saduda ba da yin ƙasa ag-wui'wa har su ajiye makamansu ga barin yaƙar musulmai.
3- Girmama harami ta hanyar barin yin yaƙi a cikinsa.
4- Har kullum burin kafuri bai wuce ya ɓullo da abin da zai cutar da musulmi ba, ba zai taɓa kawo abin da zai anfanar da su ba, idan ma akwai anfani a cikinsa to sharrinsa yafi yawa.
5- Halaccin yin yaudara da zanba cikin aminci dan kuɓuta daga shar-rin azzalumai.
6- Zalunci ba ya ɗaurewa.
7- Duk wanda ya dogara ga Allah to Allah zai isar masa.
8- Dukkan tsanani yana tare da sauƙi.

## Yaƙin Kai'bara

bayan Annabi (saw) ya danƙwafar da abokan gabarsa dake kewaye da shi aminci da kwanciyar hankali da adalci sun cigaba da wanzuwa a cikin Jazirar larabawa, sai ya rage saura daula ɗaya ta yahudawa mai ƙarfi da yalwar arziki, ita ce ƙasar Kai'bara, wacce ta tattara manya manyan yahudawa da jagororinsu, kuma idan ba ka mantaba ka san yadda suka goge suka gwanance wajen iya ƙulle ƙulle da makirce makirce da tsananin nuna ƙiyayya zuwa ga Annabi (saw) da duk wani musulmi wanda hakanne ma yasa Annabi (saw) ya koresu daga Madina, to sai labari ya isar ma Annabi (saw) cewa sun ƙulla da Gaɗafan akan za su zo su yaƙe shi, sai Annabi (saw) ya yi rigakafin haka ta hanyar haɗa rundunar mayaƙa, Annabi (saw) ya yi shela cewa kada wanda ya sake ya bisu wannan yaƙin sai mai kwaɗayin jihadi saboda Allah, sai As'habush-shajarati waɗanda suka yi Bai'atur Ridwan suka fito wanda adadinsu bai wuce mutun dubu ɗaya da ɗari huɗu ba (1400)

munafukai suka fara nasu aikin na ƙoƙarin ganin bayan musulmai ƙarƙashin jagorancin shugabansu ɗan Salul, ta yadda ya aika wa yahudawan Kai'bara shirin Annabi (saw) akansu.

Annabi (saw) ya fito tare da mayaƙansa suka doshi Kai'bara suna ta tafiya har suka kai garin da goshin magriba, sai Annabi (saw) ya dakata har gari ya waye sannan sai suka ƙarasa Kai'bara a lokacin yahudawa sun fito ƙwansu da ƙwarƙwatarsu ba su san da zuwan Annabi (saw) ba, a yayin da suka yi arba da shi, sai suka ce wallahi ga Muhammadu nan da rundunar mayaƙansa sai suka ari sawun kare

suka gudu zuwa cikin ganuwarsu, Annabi (saw) ya ce: Allahu akbar, Kai'bara ta zama kufai.

Aliyu (ra) ya ɗan samu jinkiri wajan fitowa tare da Annabi (saw) kasancewar ciwon idon da yake fama da shi, amma daga baya ya riskesa, sai Annabi (saw) ya ba shi tuta bayan ya yi masa tofi take anan ya warke kamar bai taɓa ciwon ido ba sau da ɗaya, ya umarce shi da idan ya je ya kirasu zuwaga shai'dawa babu abin bautawa bisa cancanta sai Allah kuma Muhammadu manzan Allah ne, san-nan ya sanar da su abin da Allah ya wajabta musu na daga ibadu.

Garin Kaibara ya kasance yana da ganuwowi guda takwas masu ƙarfi ƙwarai da gaske, a haka musulmai suka kutsa suka dinga tunɓukesu suna bazar dasu har aka yi galaba akansu suka mika wuya zuwa ga musulmai, Annabi (saw)  ya basu damar cigaba da zama a ƙasar bisa sharaɗin cewa duk abin da aka samu na amfanin noma to zasu ɗauki rabi ɗayan rabin kuma na Annabi ne (saw) tunda yanzu ƙasar ta zama ta Annabi (saw) domin fai'i, ce.

Haƙiƙa an samu ganima ta dabbobi da ribatattun yaƙi a wannan yaƙin na Kai'bara, daga cikin ribatattun yaƙin akwai Safiyya ummul mu'uminina ʽYar shugaban yahudawan banun-Nadir wacce jika ce ga Annabi Harun ɗan uwan Annabi Musa (saw) mijinta Abu Kinana yana ɗaya daga cikin waɗanda aka kashe daga cikin yahudawa a wannan yaƙin, to sai ta faɗo a kason Annabi (saw) sai yaʽYantata ya sanya wannanʽYantawar da ya yi mata a matsayin sadakinta.

A wannan yaƙin ma sai da yahudawa suka ɗan taɓa sana'ar tasu wacce suka yi digiri har da digir digir a kanta, wato makirci da ƙulle ƙulle, ta yadda suka samu karfata ta Tinkiya suka soyata suka sa ma

ta dafi mai ƙarfi, sai suka aikawa da Annabi (saw) da ita da yake sun san yana son karfata ta Tinkiya ko Akuya, a yayin da aka ajiye a gaban Annabi (saw) sai ya yagi tsoka ya tauna sai ya furzar ya ce: wannan ƙashin yana gaya mini cewa akwai dafi a cikinsa, sai yasa aka zo da wacce ta yi wannan aikin wato Zai'nab matar Salamu ɗan Mishkam, ta tabbatar da hakan, ya ce me yasa ki ka yi haka? Ta ce nayi hakane saboda idan ka kasance mai mulkine kai Allah zai hutashshemu daga sharrinka, idan kuma kai annabi ne to naman zai baka labarin abin da aka sa masa na dafi, daga cikin waɗanda suka ci wannan naman akwai Bara'u ɗan Ma'arur, wanda take anan ya mutu.

**Darussa:**

1- Babu wani abu da yake samuwa cikin sauƙi sai an yi gwagwarmaya a kansa, ka duba yadda Annabi (saw) ya ke ta faɗi tashi wajen ganin ya tabbatar da daular Musulunci, wanda inda Allah ya so a rana guda komai zai tabbata, amma sai hakan bai faruba don a nuna maka komai sai an yi gwagwarmaya da faɗi tashi wajen tabbatar da shi.
2- Ka fara ɗaukan mataki akan makashin ka kafun ya ɗauki nasa matakin akan ka.
3- Bayahude ba zai taɓa canzawa ba.
4- Adalcin Musulunci ta yadda Annabi (saw) ya tabbatar da su akan su cigaba da zama a cikinta.

## Yaƙin fathu Makka

bayan yaƙin kai'bara komai ya daidaita ta yadda aka dakushe kaifin takobin abokan gabar addinin Allah ya zamto kowanne jinsi daga

cikin abokan gabar Musulunci yana jin shakkar ya kawo masa wargi, sai Allah ya yi nufin tabbatar da tamkini ga musulmai a faɗin jazirar larabaya gaba ɗaya ta hanyar murƙushe manyan abokan gabar Annabi (saw) waɗanda suka kore shi daga garinsa gaba ɗaya, domin sune mafi girman barazana ga daular Musulunci a wannan lokacin a cikin Jazira.

idan ba ka mantaba a baya ka ji irin yarjejeniyar da aka ƙulla tsakanin ƙurai'shawa na tsagaita wutar yaƙi tsakaninsu da musulmai na tsawon shekara goma, kuma duk ƙabilar da take so ta marawa kowane ɓangare baya tana da damar hakan, amma idan aka samu wata ƙabila daga cikin ƙabilun da suka marawa wani ɓangare baya ta yi ta'addanci ga ɗayar ƙabilar to kamar ta yiwa wannan ɓangaren ta'addancine, a inda ƙabilar Kuza'a ta marawa Annabi (saw) baya ƙabilar banu Bakar kuma suka marawa ƙurai'shawa baya, to sai ƙabilar banu Bakar suka yi ta'addanci ga ƙabilar Kuza'a, ƙurai'shawa kuma suka taimaka musu da makamai akan Kuza'a, to wannan shine dalilin yaƙin fathu Makka domin warware wannan alƙawarin da ƙurai'shawa suka yi.

To yayin da ƙurai'shawa suka yi wannan aika aika ba tare da tunanin abin da ka iya zuwa ya dawo ba, sai kuma suka tsorata suka gaggauta tura Abu Sufyan zuwa ga Annabi (saw) don ƙara jaddada masa suna nan akan wannan yarjejeniyar, amma Annabi (saw) bai ce masa kanzil ba, haka ya je wajen Abubakar don kamun ƙafa nan ma bai yi nasaraba, hakama abun ya kasance a wajen Umar da Aliyu.

Annabi (saw) ya shirya gagarumar runduna ta mayaƙa waɗanda adadinsu ya kai dubu goma (10,000) dan tunkarar Makka.

A yayin da Annabi (saw) yake shirye shiryen fita sai Haɗibu ɗan Abi Balta'ata ya rubuta takarda zuwa ga ƙurai'shawa yana sanar dasu zuwan Annabi (saw) ya ba wata mata ta ɓoye a cikin kitson ta dan ta isar ma da ƙurai'shawa, har ta fita ta fara tafiya sai Allah ya saukar da wahayi yana bayyana wa Annabinsa (saw) shirin Haɗibu, sai Annabi (saw) ya tura Aliyu da Zubai'ru suka je suka tareta suka sa ta fito da wannan wasiƙar suka kawoma Annabi (saw)
Wanda shi Haɗibu ya yi hakanne ba dan munafunciba ko dan a cutar da Musulunci ba, a a ya aikata hakanne akan kuskure, bisa dogaro da cewa Ƴaƴansa da dukiyarsa suna hannun ƙurai'shawa, daga ƙarshe Annabi (saw) ya mai uzuri kuma ya hana a tsangwame shi domin yana daga cikin waɗanda suka halarci yaƙin Badar.
Annabi (saw) ya fito ya doshi Makka da shi da zaƙwaƙwuran dakarunsa kimanin su dubu goma (10,000) har suka kai wani waje da ake kira da ƙudai'd, wanda tsakaninsa da Makka tafiyar kilo mita cassa'in (90) ce, suka yada zango daman sun fito da A zumi a bakinsu sai suka ajiye shi suka sha ruwa a wannan wajen, daga nan suka ɗaga suka cigaba da tafiya, sai suka haɗu da Abbas baffan Annabi (saw) tare da iyalansa yana nufin Madina, daman ya riga ya musulunta.
Annabi (saw) ya iso Makka da isha'i, sai ya yada zango a Marrizzahran, ya sa aka kunna wuta har kashi dubu goma dan firgitar da ƙurai'shawa, kuma cikin hikimar Allah sai aka ɓoye musu labarin zuwan Annabi (saw) balle har su ɗau wani ƙwaƙƙwaran mataki akan hakan, wanda kafun a ƙarasa shiga Makka suka haɗu da Abu Sufyan akan hanya, daga nan ya musulunta ya kyautata musuluncinsa.
Daga nan aka kutsa cikin Makka, sai Abu Sufyan ya ɗaga murya yana cewa: ya ku taron ƙurai'shawa ga Muhammadu nan ya zo muku da

wata bataliyar runduna wacce ba za ku iya tunkararta ba, daman Abu Sufyan ya ce ma Annabi (saw) ya yi masa wani abu wanda zai faranta masa rai ya yi alfahari da shi, domin shi mutunne mai son abun alfahari, sai Annabi (saw) ya ce duk wanda ya shiga gidan Abu Sufyan to yana cikin aminci, to sai Abu Sufyan ya ci gaba da cewa ƙurai'shawa: duk wanda ya shiga gidan Abu Sufyan to yana cikin aminci, duk wanda ya shiga masallacin Harami yana cikin aminci duk wanda ya kulle ƙofarsa yana cikin aminci, matarsa ta so ta kawo masa tangarɗa, daga nan dai mutane suka shige gidajensu wasu kuma masallaci wasu kuma gidan Abu Sufyan.
Can sai ga rundunar musulmai ta durfafo Makka kai kace mutanen duniya ne suka taru gaba ɗaya saboda kwarjininsu, waɗanda gigin hau'ka ya ɗebesu suka kawo wargi take ake murƙushesu.
Daga nan Annabi (saw) ya shiga cikin Masallacin Harami ya sumbaci Hajarul Aswad ya yi ɗawafi a ɗakin Allah mai alfarma. a zagaye da Ka'aba akwai gumaka kimanin ɗari uku da sittin (360) adadin kwanakin shekara, Annabi (saw) yasa sanda yana zungurinsu yana cewa: gaskiya ta zo ƙarya ta ruguje, lallai ƙarya ta kasance rusas-shiya. Duk gunkin da ya zungura sai ya faɗi ya karye, daga nan sai ya amshi makullin Ka'aba a hannun Usman ɗan Ɗalha, ya shiga cikin Ka'aba ya tarad da wani gunki a cikinta wanda aka sassaƙa a bisa sura ta Annabi Ibrahim da ɗansa Annabi Isma'il (as) a hannuwansu akwai kibbau na caca gasu nan suna caca, Annabi (saw) ya ce: Allah ya la'ancesu Annabi Ibrahin da ɗansa basu taɓa cacaba, daga nan ya yi salla raka'a biyu.
Bayan wannan gagarumin fathin da Allah ya yi wa Annabinsa (saw) wanda ya ƙasƙantar da ƙarfin kafirci ya ma kashe shi gaba ɗaya, ya ɗaukaka daular Musulunci, yau ga Annabi (saw) a cikin garinsa

wanda ya fita a fakai'ce a ɓoye don gudun ƙurai'shawa, yau gasu nan a ƙasƙance a gabansa, wannan yana daga cikin ƙudirar Allah jalla wa'ala.

Daga nan sai ƙurai'shawa suka jaddada mubaya'arsu ga Annabi (saw), sannan ya zauna a Makka tsawon kwana goma sha tara yana karantar da musulman da suka karɓi Musulunci a wannan yaƙin.

**Darussa:**

1- Yadda muka ga Musulunci yana ci gaba yana burunƙasa a koda yaushe, ta yadda idan aka fita wannan yaƙin da wani adadi na sahabbai sai ka ga adadin ya ƙara ƙaruwa a karo na daban.

2- Bayyana ƙarfin Musulunci na makamai da na yawan sojoji da makamancin haka.

3- Girmama mai wani matsayi a cikin mutanensa, ta hanyar yi masa abin da zai ƙara tabbatar da matsayinsa kamar yadda Annabi (saw) ya yi wa Abu Sufyan.

4- Karamcin Annabi (saw) ta yadda ya yafe ma ƙurai'shawa tare da irin tsananin cutarwarsu gareshi da yunƙurin kasheshi fiye da sau shurin masaƙi, wanda sun cancanci ya kashesu, amma saboda karamci irin na Annabi (saw) sai ya yi musu afuwa.

5- Dukkan tsanani yana tare da sauƙi, kuma rashin nasara yana tare da nasara, amma duk wannan baya tabbata sai da haƙuri.

6- ƙara tabbatar da gaskiyar manzancin Annabi (saw) da kuma nun-awa duniya cewa addinin Musulunci shine addinin gaskiya kuma shine addinin Allah, ta yadda Allah ya danƙwafar da dukkan wani addinin da ya yi fito-na-fito da shi, ya ɗaura Musulunci akansa.

7- A faɗi a tashi ko bajima ko badaɗe gaskiya ita ce a sama ƙarya a ƙasa.

## Yaƙin Hunai'ni

Bayan wannan gagarumar nasara da tamkinin da Allah ya yi wa annabinsa (saw) na fathu Makka, ya kasance hatta ƙasashen ƙetare sun sha jinin jikinsu game da daular Musulunci, to agefe ɗaya kuma akwai wasu tsageru daga cikin ƙabilun Larabawa waɗanda su ba su ɗau izina ba akan abin da ya faru ga babbar daular kafurci ta cikin gida, waɗannan ƙabilun sune Hawazin da Saƙif da makamantansu ƙarƙashin jagorancin Malik ɗan Auf, ta yadda izza ta ɗaukesu suka tara rundunar mayaƙa da zummar yaƙar Annabi (saw) bisa ruɗin sheɗan, suka tattaro matayensu da dukiyoyinsu suka tasasu agaba suka doshi Madina dan yaƙar Annabi (saw) suka yada zango a wani waje da ake kira da kwazazzabon Auɗas.

A can Madina kuma labari ya isar ma Annabi (saw) cewa ga Hawazin nan da Saƙif da wasu daga cikin ƙabilun Larabawa sun tinkaro Madina dan su yaƙe shi, wannan ya farune a shekara ta takwas bayan hijira (8)

Annabi (saw) ya yi shiri ya haɗa rundunar mayaƙa kimanin mutun dubu goma sha biyu (12,000) mutun dubu goma sune waɗanda suka fito fathu Makka tare da shi, mutun dubu biyu kuma sune waɗanda suka musulunta daga mutanan Makka, daman Annabi (saw) ya tura Abu Hadrad Al'aslami zuwa ga abokan gaba domin ya binciko sirrinsu.

A hanyar zuwa hunai'ni ne wasu daga cikin sabbin musulunta suka ga wasu mutane suna bautawa wata itaciyar Magarya, sai suka ce da Annabi (saw) suma ya sanya musu irin wannan itaciyar ta zama

tsani garesu zuwa ga Allah! Annabi (saw) ya yi kabbara ya ce: wannan Magana taku kwatankwacin abin da banu Isra'ila suka ce da annabi Musa ne a yayin da Allah ya tsiratar dasu daga sharrin Fir'auna.

Ba a gusheba ana ta tafiya har aka kai sansanin da abokan gaba suka yada zango, daman shugaban abokan gaba Malik ya tura ɗan leƙen asiri dan ya gano musu shirin musulmai, sai ya dawo abirkice ya ce: haƙiƙa na ga mazaje iya ganin mai gani akan dawakai masu ratsin baƙi da fari, gaba ɗaya sai suka firgita suka razana.

To daman Malik ya riga ya kama cikin kwazazzabon da kuma duhuwowi ya umarci dakarunsa da su ɓoɓɓoye a cikin duhuwowin suna ganin musulmai sun nufosu su fara antaya musu ruwan kibbau sannan su afka musu gaba ɗaya, aikuwa haka aka yi, domin musulmai suna zuwa suka fara musu ruwan kibbau wanda hakan yasa musulmai suka juya da baya suka watse, har wasu daga cikin sabbin musuluntar nan suka fara faɗin maganganu marasa daɗi, amma duk da kasancewar wannan halin da musulmai suka faɗa wannan bai sa Annabi (saw) da Abubakar da Umar da Aliyu da Abbas sun yi ko gezau ba, bal, suna nan atabbace, Annabi (saw) ya shiga kiran mutane yana cewa ku dawo, ya sa amminsa Abbas da ya yi shela ya kira mutane, da yake yana da amon sauti sosai, ya shiga yana kiransu suka amsa suna labbaika labbaika, sahabbai suka daddawo.

dalilin da ya jawo wannan rashin nasarar a farkon haɗuwa shine alfaharin da sahabbai suka yi ta yadda suka ce ayau dai kam ba za a rinjayemu ba saboda ƙarancinmu, sun manta da cewa Allah ne

mai basu nasara a koda yaushe, sun manta da ranar Badar, sun manta da ranar Ahzab.

Bayan sahabbai sun dawo sai aka cigaba da gumurzu, Annabi (saw) ya ɗebi ƙasa ya watsama kafurai ya ce: na rantse da ubangijin Muhammadu (saw) sun karye sun watse. ba a daɗe ba ana ɗauki ba daɗi ba alƙaluma suka sauya ma'aunai suka jujjuya Allah ya ba musulmai nasara akan abokan gabarsu, suka kashe na kashewa suka kama na kamawa masu gudu suka gudu, wan nan tarin dukiyar tasu da suka fito da ita dan ta ƙara musu ƙarfin gwui'wa sai ta zama ganima ga musulmai, wanda adadin ribatattun yaƙin ya kai dubu shida (6,000) raƙuma dubu ashirin da huɗu (24,000) tumakai sama da dubu arba'in (40,000) tsabar kuɗi na Azurfa Uƙiya dubu huɗu (4,000) wanda ƙimarsu a lissafin wannan shekara (1442)h (2021)m ta kusa kai biliyon biyu (2,000,000,000) amma duk da tarin dukiyar nan Annabi bai ɗauki wani abu a cikinta ba, bal, sai ma ya rarrabawa sababbin musulunta domin a ƙara tabbatar da diga digansu akan imani, ya ɗauki raƙuma ɗari ya ba wancan haka dai ya rabar da ita ga waɗannan mutanen gaba ɗaya, hatta Al'ansar bai basu komai daga cikin ta ba.

A cikin kamammun nan kuwa akwai Shema'u 'Yar'uwa ga Annabi (saw) ta shayarwa, ta bayyana ma annabi (saw) kanta ya ganeta ya karramata ya shimfiɗa mata mayafinsa yai ma ta sha biyu ta arziƙi ya sa aka maida ita zuwa ga mutanenta.

Su kuma ƙabilun Hawazin sai suka rankayo gaba ɗayansu zuwa ga Annabi (saw) a matsayin musulmai.

**Darussa:**

1- ƙarshen tika-tika tik, da wannan yaƙinne Allah ya kawo ƙarshe abokan hamayya masu son su ga ƙarshen musulunci a cikin Jaziratul Arab, Allah ya cikama annabinsa alƙawarin da ya yi masa na ba shi tamkini a bayan ƙasa.
2- Allah baya son alfahari da jiji da kai, a a duk abin da ka samu na nasara to ka jinginashi zuwa ga Allah.
3- Alfahari baya haifar da ɗa mai ido.
4- Annabi (saw) ba dan ya tara abun duniya ya ke yaƙiba, bal, asali ma baya yaƙi sai an takaleshi.
5- Yana da kyau mutun ya girmama zumunta ta hanyar kyautata ma ɗan'uwansa koda ba musulmi bane kuma koda ba ɗan,uwansa ba ne na jini.

## Yaƙin Tabuka

Wannan yaƙin shine yaƙi na ƙarshe a rayuwar Annabi (saw) Tabuka wani garine dake arewacin masarautar Sa'udiya, dalilin wannan yaƙin shine kasancewar daular Rum tana ɗaya daga cikin dauloli guda biyu mafi girma da ƙarfi a faɗin duniya gaba ɗaya a wannan lokacin, wato ita da Faris, kamar ka ce: Amerika da Ingila da Rasha da Faransa a yanzu, to kusan duk garuruwan Larabawa a ƙarƙashin ikon Rumawa suke, to ganin yadda Annabi (saw) ya mamaye waɗannan birane na cikin yankin Larabawa gaba ɗaya, sai ƙai'sar ya firgita ya ji tsoron kada su mai tawaye tinda daman suna fatan ganin samun 'Yancin kai ga kuma dama ta samu, sai ya haɗa gagarumar runduna har da ta haɗin gwuiwar larabawan da suke maƙobtaka da shi, wanda adadin mayaƙan da ya tara sun tasamma dubu arba'in (40,000)

A yayin da labari ya riski Annabi (saw) sai ya shiga kwaɗaitar da sahabbai (rah) akan jihadi saboda ciyar da addinin Allah gaba, wanda wannan labarin ya riskeshi ne a lokacin da ake cikin tsananin zafi da ƙarancin abun hannu, ga tafiya kuma mai nisan gaske wacce ba a taɓa yin kwatankwacinta ba, gashi kuma  anfanin itatuwa sun nuna.

Amma duk da haka sahabbai ba su yi ƙasa agwui'wa ba haka suka sallama jin daɗinsu da hutunsu don ɗaukaka addinin Allah ta'ala, tsantsar imanin sahabbai (rah) ya kuma bayyana a wannan lokacin, masu wadata suka yi abin da tarihin ɗan Adam bai taɓa shai'dar kwatan kwacinsa ba, ta yadda Abubakar ya bada dukiyarsa gaba ɗaya fisabilillah, adadin ta kuwa ya kai dirhami dubu huɗu (4,000) dai dai da miliyon arba'in da 'Ya'Ya (40,00000) Umar kuma ya bada rabin dukiyarsa, Usman kuma babban attajiri kusan shine ruhin yaƙin ta fiskar taimakawa, domin ya bada gudummuwar raƙuma ɗari tara (900) da dawakai ɗari (100) da kuɗaɗe masu tarin yawa, manzan Allah (saw) ya ce: duk abin da Usman ya aikata na kuskure to ba zai cutar da shi a wajen Allah ba, wannan isharace zuwaga cewa ba zai aikata wata kaba'ira ba, shi kuma Abdurrahmanu ɗan Aufu ya bada Uƙiya ta Azurfa ɗari biyu, wato dirhami dubu huɗu (4,000) haka dai kowa ya dinga kawo gwargwadon abin da Allah ya hore masa, wani ya kawo buhunan dabinu wani buhu ɗaya wani kwano ɗaya wani mudu ɗaya, kowanne gwargwadon iyawarsa, mata ma ba a bar su a baya ba, suka dinga cire ɗankunnayensu da sarƙoƙinsu da awarwarayensu suna badawa saboda Allah, munafukai suka shiga zunɗen masu sadaka, idan mutun ya bada mai yawa sai su ce dan riya ya yi, idan ya bada kaɗan sai su ce me Allah zai yi da wannan.

Sahabbai da dama suka yi ta zuwa wajen Annabi (saw) akan ya basu abun hawa domin ayi wannan tafiyar dasu, idan akwai ya basu idan kuma babu sai ya basu haƙuri, sai su yi baƙin ciki da hakan wasu ma su yi kuka, su kuma munafukai awannan lokacine kasuwarsu ta buɗe suka dinga sharara ƙarya da kawo uzururruka na ƙarya dan Annabi (saw) ya ba su izinin zama ba sai an fita dasu ba, wani ya ce matarsa bata da lafiya, wani kuma ya ce katangar gidansa ta faɗi da dai zantuttuka irin waɗannan marasa kan gado.

Haka Annabi (saw) ya gama haɗa rundunar mayaƙansa suka kama hanya zuwa Tabuka, wanda adadin dakarun da aka fita dasu a wannan yaƙin sun kai dubu talatin (30,000) wanda ba a taɓa fita da irin wannan adadin ba aduk yaƙoƙin da Annabi (saw) ya halarta a rayuwarsa.

Haka dai aka kama hanya ana inba-kayi bani-wuri a kwana anan a tashi acan a yada zango anan, duk da irin gudummuwar da attajiran sahabbai suka bada wannan bai gamsar da rudunarba don yawansu, domin mutun goma sha takwas sun kasance suna yin tarayya akan raƙumi guda, idan wannan ya hau ya yi adadin tafiya kaza sai ya sauka ya ba wannan, wani lokaci ma ganyen bishiya ne abincinsu wani sa'in kuma sukan yanka raƙumi domin su sha ruwan da ya ke Tarawa a ma'ajiyar ruwansa, a haka dai aka yi ta tafiya wanda abubuwa daban daban na ban al'ajabi sun faru akan hanya wanda littafin ba zai isa ace an kawo maka komai da komai ba, har aka isa Tabuka, a yayin da Rumawa suka ji labarin zuwansa sai suka razana suka gudu, Annabi (saw) ya tsaya a Tabuka tsawon kwana goma sha wani abu, a wannan tsakanin ne sarakunan dake wannan yankin suka yi ta zuwa neman sulhu suna bada Jizya, kamarsu

sarkin Ai'lata da mutanan Jarba'u da na Azruh, daga nan sai Annabi (saw) ya juyo zuwa Madina, a yayin da duniya ta gama girgiza da lamarinsa.

**Darussa:**

1- Haƙiƙa wannan yaƙin shine mafi girman yaƙoƙin Annabi (saw) wanda ya ƙara bayyana wa Duniya gaskiyar abin da ya zo da shi na shiriya, kuma ya ƙara tabbatar ma ta da kafuwar daular Musulunci kafuwar da tunɓuke ta ba zai yiwu ba, ta yadda har ƙasa mai ji da kanta wacce Duniya take ganin karanta ya kai tsai'ko kuma ake jin shakkarta, idan ta dubi gabas ta ce yamma ba wanda zai ce ba hakaba ne, amma yau gashi sun kasa yin gaba da gaba da rundunar Musuluncin da ake gani sune maƙasƙanta a da.

2- Tsananin ƙarfin imanin sahabbai da kuma yadda suke rayuwa dan wannan addinin ba dan su ci ba ko su sha.

3- Addinin Allah baya tafiya yadda ya kamata sai da kuɗaɗen da za a dinga anfani dasu wajen tafiyar da shi.

4- Musulmai su suke ɗaukar ragamar tafiyar da addininsu ta hanyar bada gudummuwa domin ciyar da shi gaba ba tare da nema daga wani bare ba.

5- Kada ka rai'na ɗan abin da za ka yi sadaka da shi, duk abin da Allah ya hore maka to ka bada kada ka rai'na, domin abin da Allah ya hore maka komai ƙanƙantarsa to mai yawane a wajen Allah.

6- Da ba dan sahabbai ba da wannan addinin ba inda zai je, domin sune suke faɗi-tashi da jininsu da dukiyarsu wajen ganin tabbatuwarsa, saboda haka duk wani musulmi a yau a duk inda yake a

faɗin Duniya arzikinsu ya ke ci, idan ya yi musun hakato dama ba addinin Musulunci ya ke yi ba wani addinin ya ke yi can na daban.

Bayan wannan yaƙin na Tabuka ne ƙabilu daban daban suka dinga yin ayari suna zuwa wajen Annabi (saw) suna shiga Musulunci.

## Rashin lafiyar Annabi (saw) da wafatinsa

Bayan Allah ya tabbatar da da'awar Annabi (saw) ya rinjayar da ita akan kowacce da'awa, ya cika masa burinsa, Annabi (saw) ya yi aikin hajjinsa na bankwana! Wanda shine nafarko kuma naƙarshe, domin sau ɗaya ya taɓa aikin hajji a rayuwarsa, Annabi (saw) ya dinga yin bankwana da duk wani muhimmin abu da yake da alaƙa da shi, ya je Uhdu ya yima shahidai sallah ta bankwana, ya shiga maƙabartar Baƙi'a ya yima mamatanta addu'a ya nema musu gafara.

Daga nan sai ya fara rashin lafiya, wanda hakan ya farune ranar Litinin ashirin da tara ga watan Safar, daga nan ciwo ya ci gaba da tsananta ga Annabi (saw) har ya kasance cewa baya iya fita sallah, sai ya umarci Abubakar da ya yiwa mutane sallah, Annabi (saw) ya yi wa sahabbai wasiyoyi da abubuwa daban daban waɗanda dukkannin su akan kula da Addinine da kuma kiyaye daular Musulunci da makamantan hakan.

Da hantsin ranar Litinin ne ranar sha biyu ga watan Rabi'ul Au'wal a shekara ta sha ɗaya da yin hijira shekara ta ashirin da uku da annabci wata gagarumar musiba ta sauka ga Duniyar Musulunci wacce ba a taɓa yin kamarta ba kuma ba za a kara maimaita kwatankwacinta ba, wannan musibar ita ce komawar Annabi (saw) zuwaga Allah! haƙiƙa wannan ba ƙaramar musiba ba ce da tashin hankali ga duk wani musulmi wanda sha'anin Addini yake gabansa, domin hatta sahabbai duk da ƙarfin imaninsu sai da da yawansu suka ruɗe har Umar ya ke cewa Annabi (saw) bai rasu ba kuma duk wanda ya ƙara cewa Annabi (saw) ya rasu to zai sare masa kai, har

sai da Abubakar ya zo ya daidaita nutsuwar mutane ya tabbatar musu da rasuwar Annabi (saw) ta hanyar karanto ayar da take nuna cewa Annabi (saw) zai koma ga Allah ko bajima ko badaɗe, Annabi (saw) ya rasune a jikin A'isha a tsakanin ƙirjinta.

Daga nan sahabbai suka yi masa wanka ba tare da an cire masa tufafinsa ba, aka lulluɓeshi da likafani guda uku, sannan kowannensu ya yi masa sallah a karan kansa ba tare da an yi masa jam'i ba kamar yadda aka saba yi wa mamaci sallah, sannan sai suka yi saɓani akan inda yakamata abinne shi, sai Abubakar ya ce: na ji Annabi (saw) yana cewa: duk Annabin da ya yi wafati to ana binne shi ne a inda ya yi wafati, sai aka binne shi anan ɗakin A'ishatu (ra)

Annabi sallallahu alaihi wa sallam ya rasu yana da shekaru sittin da uku (63)

## Siffofin Annabi (saw) da Kyawawan ɗabi'un sa

Haƙiƙa Annabi (saw) shine mafi cikar mutane halitta mafi kamala mafi kyawun fuska da haske da annuri da kwarjini, shi ba dogo bane talala, kuma ba gajere bane ya na tsakankanin hakan, kuma ba wanda yake ƙere shi a tsawo idan sun jera da shi, wannan mu'ujizarsa ce, sannan shi ba fari bane kamar zabaya, kuma shi ba ja bane kuma shi ba baƙi bane kuma shi ba wankan tarwaɗa bane, sannan gashin kansa ba a dunƙule yake ba, a a laya-laya ne gwanin ban sha'awa, sannan kan shi babbane ba can sosai ba, sannan yana da manyan zira'i da damatsa alamun sadauki ne jarumin gasken gaske, bai taɓa juyawa da baya ba a fagen Daga, sannan yana da yalwar idanu masu matuƙar fari sannan baƙin dake cikinsu baƙine ƙwarai da gaske, idan ya na tafiya ba ya yin irin ta ragwaye ya na

jan ƙafa, a a idan ya na tafiya kai ka ce ya na sakkowa daga kan tudune, kuma ya na tafiya a tsanake ba sauri mara kan gado ba ba kuma tafiyar ragwayeba, amma duk da haka idan sahabbai suka jera da shi sai suna ɗan haɗawa da gudu gudu, wannan ya na daga cikin mu'ujizarsa.

idan muka koma zuwa ga batun kyawawan ɗabi'u da mu'amaloli, wannan kuma wani abune wanda ya shige tunanin mai tunani da hasashen mai hasashe, domin Annabi (saw) ya tattara duk wata kyakkyawar ɗabi'a wacce kowane mutun ya siffanta da ita har ma da ɗoriya, ya na da matuƙar kamewa da juriya da haƙuri da kyauta da karamci masu rikitar da wanda aka mawa, wanda hat takai yana ma yara ƙanana sallama akan hanya, ya na taya iyalansa hidindimunsu na gida, wajen cika alƙawari kuwa ba a Magana, domin ya fi kowa cika alƙawari da riƙe amana, haƙiƙa kyawawan ɗabi'un Annabi (saw) da halayensa sun fi gaban a bayyanasu haƙiƙanin bayyanawa, sai dai kawai mutun ya faɗi abin da zai iya faɗa, Allah ya bamu ikon yin koyi da shi.

## Matayensa iyayen muminai

Annabi (saw) ya auri mata goma sha uku, ya tare da sha ɗaya ya rasu ya bar guda tara, guda biyu kuma sun rasu tun ya na da rai, sune: Kadija, da Zai'nab'Yar Kuzai'ma. auren sama da mata huɗu ya na daga cikin abubuwan da suka halatta ga Annabi (saw) shi kaɗai ba wanda ya yi tarayya da shi a cikin musulmai akan hakan, ga sunayen matayen nasa kamar haka:

1- Kadijatu ʼYar Kuwaiʼlid (ra) ita ce matarsa ta farko kuma uwa ga ʼYaʼYayensa gaba ɗaya ban da Ibrahim, bai ma ta kishiyaba har ta koma zuwa ga Allah.
2- Sauʼdatu ʼYar Zamʼatu (ra) ita ce wacce ya fara aura bayan Kadija.
3- Aʼishatu ʼYar Abubakar Assiddiƙ (ra) ita ce kawai budurwa acikin matan da ya aura, ya aureta ta na da shekara shida, ya tare da ita tana ʼYar shekara tara.
4- Hafsatu ʼYar Umar ɗan Kaɗɗab (ra) ʼYa ga Amirul muʼuminina Umar ɗan Kaɗɗab (ra)
5- Zaiʼnab ʼYar Kuzaiʼma (ra) mamar miskinai, ba ta daɗeba ta rasu.
6- Ummu Salma Hindu ʼYar Abi Umayya (ra) mahaifiyar Anas ɗan Maliku (ra)
7- Zaiʼnab ʼYar Jahshin (ra) ita ce wacce Allah ya ɗaura aurenta da Annabi (saw) daga saman bakwai.
8- Juwaiʼriyya ʼYar Haris (ra) ta na ɗaya daga cikin ribatattun yaƙin banu Musɗaliƙ, sai Annabi (saw) ya ʼYantata ya aureta.
9- Ummu Habiba Ramla ʼYar Abu Sufyan (ra) Annabi (saw) ya aureta ne a yayin da ta yi hijira zuwa Habasha tare da mijinta Ubaiʼdul-lahi ɗan Jahshin, sai ya yi ridda, sai Annabi (saw) ya turo ya na neman aurenta a wajen Najashi kamar yadda ya gabata.
10- Safiyya ʼYar Huyayyu ɗan Akɗabu (ra) ta kasance ʼYa ga shuga-ban yahudawan banun-nadir, kuma ɗaya daga cikin ribatattun yaƙin Kaiʼbara, sai Annabi (saw) ya ʼYantata ya aureta.
11- Maiʼmunatu ʼYar Haris (ra) Annabi (saw) ya aureta bayan ya kammala aikin umara ta ramako a bisa zance mafi ƙarfin dalili.

Amma ƙwarƙwarorinsa guda biyu ne: 1- Mariyatul Kibɗiyatu, ita ce ta Haifa masa Ibrahim (ra) 2- raiʼhanatu ʼYar Zaiʼdu, ta kasance ɗaya daga cikin ribatattun yaƙin banu ƙuraiʼza.

## ƳaƳayen Annabi (saw)

Allah  ya azurta Annabi (saw) da ƳaƳaye guda bakwai, maza uku mata huɗu, amma ba wanda ya rayu daga cikin mazajen bisa wata hikima ta Allah, ga sunayensu nan kamar haka:

1- Alƙasim (ra)  2- Abdullahi (ra)  3 – Ibrahim (ra)

4- Faɗimatu (ra) ita ce mafi soyuwa daga cikin ƳaƳansa (saw), kuma ita ce uwa ga jikokin Annabi (saw), Aliyu ɗan Abu Ɗalib (ra) shine mijinta, ita ce mafi tsawon rayuwa daga cikin ƳaƳansa (saw) wacce ta rayu bayan ransa.

5- Ummu kulsum (ra) Usman ɗan Affan (ra) shine mijinta, ba ta daɗe a wajensa ba ta rasu.

6- Ruƙayya (ra) ita ma Usman ne ya aureta bayan rasuwar Ƴar'uwatta Ummu kulsum.

3- Zai'nab (ra) ita kuma Abul As ɗan Rabi'a ne ya aureta kafun hijira, daga nan musulunci ya rabasu, sannan kuma ya ƙara haɗasu da wan nan auren nasu na farko.

## kullewa

Wannan shine abin da na ga ya kamata in kawo game da tarihin Annabi (saw) cikin harshen Hausa a taƙaice, domin ʽYan'uwammu masu magana da wannan harshen su amfana da shi su san Annabinsu (saw) su ɗabbaƙa karantarwarsa akan su, kuma su yi koyi da shi, domin mutanenmu suna ƙaunar Annabi (saw) matuƙa, to ya na daga cikar ƙaunar da kake wa mutun ka san tarihinsa ka san shi waye da irin gwagwarmayar da ya yi a rayuwarsa, da kuma kyawawan ɗadi'un sa da halayensa, wannan sai ya ƙara maka sonsa da ƙaunarsa da kuma son tafarkinsa, domin wannan shine maƙasudin karanta tarihin Annabi (saw) ba wai a karanta dan nishaɗi ba kawai.

Na fara aikin wannan littafine a lokacin ina da ayyuka masu tarin yawa na wasu rubuce rubucen, da yawan zirga zirga, amma saboda mahimmancin wannan maudu'in haka na daure na ke taɓawa har Allah yasa na kammala, wanda na fara a ashirin da shida ga watan takwas watan Hijira (28 – 8 1442)h wanda ya zo dai dai da takwas ga watan huɗu a lissafin Nasara (8 – 4 – 2021) na kammala aranar Lahadi (18 – 10 – 1442)h (31 – 5 – 2021)m

ina roƙon Allah da ya amfanar da shi ga waɗanda aka yi dominsu, ya kuma sa mun yi dan neman yardarsa ya sanya mana shi a cikin kyawawan ayyukan mu, lallai shi maji roƙone kuma mai amsa kiran mai kirane.

**ɗan'uwanku a Musulunci**

**Abu Zakariyya Arrigasi**

# قَائِمَةُ الْمَرَاجِعِ

## Jerin littattafan da aka yi muraji'arsu

1. القرآن الكريم.

2. صحيح البخاري.

أبو عبد الله محمد بن إسماعيل بن المغيرة البخاري – دار الفجر للتراث – ترقيم محمد فؤاد عبد الباقي.

3. صحيح مسلم.

أبو الحسين مسلم بن الحجاج بن مسلم القشيري – دار الفجر – الطبعة الثانية، تخ: 1434هـ.

4. سنن أبي داود.

سليمان بن الأشعث بن إسحاق بن بشير السجستاني الأزدي – دار ابن الهيثم.

5. سنن الترمذي.

أبو عيسى محمد بن عيسى بن سورة الترمذي ـ دار الفجر للتراث ـ الطبعة الثانية ـ تخ: 1434هـ.

6. سنن النسائي المجتبى.

أحمد بن شعيب النسائي – المكتبة التوفيقية – الطبعة الثانية – تخ: 2014م

7. سنن النسائي الكبرى.

المؤلف السابق – تحقيق حسن عبد المنعم سلبي – مؤسسة الرسالة – الطبعة الأولى – تخ: 1421هـ

8. سنن ابن ماجه.

أبو عبد الله محمد بن يزيد بن ماجه القزويني – تحقيق محمد فؤاد عبد الباقي – دار إحياء الكتب العربي.

9. موطأ الإمام مالك.

أبو عبد الله مالك بن أنس بن أبي عامر الحميري المدني – شركة القدس القاهرة.

10. سنن الدارمي.

أبو محمد عبد الله بن عبد الرحمن بن الفضل بن بهرام الدارمي – تحقيق حسين سليم أسد الداراني – دار المغني – الطبعة الأولى – تخ: 1412هـ.

11. سنن الدارقطني.

أبو الحسن علي بن عمر بن أحمد بن مهدي الدارقطني – تحقيق شعيب الأرنؤوط – مؤسسة الرسالة – الطبعة الأولى – تخ: 1424هـ.

12. السنن الكبرى.

أحمد بن الحسين بن علي بن موسى الخراساني البيهقي – تحقيق محمد عبد القادر عطا – دار الكتب العلمية – الطبعة الثالثة – تخ: 1424هـ

13. المستدرك على الصحيحين.

أبو عبد الله الحاكم بن محمد بن عبد الله بن حمدويه النيسابوري – تحقيق مصطفى عبد القادر عطا – دار الكتب العلمية – الطبعة الأولى – تخ: 1411هـ.

14. مغازي الواقدي.

أبو عبد الله محمد بن عمر بن واقد السهمي الأسلمي الواقدي – تحقيق مارسدن جونس – دار الأعلمي – الطبعة الثالثة: 1409هـ.

15. تاريخ خليفة بن خياط.

أبو عمار خليفة بن خياط بن أبي هبيرة الأخبري.

16. تاريخ الأمم والرسل والملوك.

أبو جعفر محمد بن جرير بن يزيد بن كثير الطبري الآملي – دار التراث – الطبعة الثانية: 1387هـ.

17. الطبقات الكبرى.

أبو عبد الله محمد بن سعد بن منيع الهاشمي البغدادي – تحقيق زياد محمد منصور، مكتبة العلوم والحكم – الطبعة الثانية: 1408هـ.

18. الاستيعاب.

أبو عمرو يوسف بن عبد البر النمري الأندلسي – تحقيق محمد البِجاوي – دار الجيل، الطبعة الأولى: 1412هـ.

19. أسد الغابة.

أبو الحسن علي بن محمد بن محمد بن الأثير الشيباني – تحقيق علي محمد معوض، دار الكتب العلمية – الطبعة الأولى: 1415هـ.

20. عيون الأثر.

أبو الفتح محمد بن محمد بن سيد الناس اليعمري – دار القلم – الطبعة الأولى: 1414هـ.

21. تاريخ ابن خلدون.

أبو زيد عبد الرحمن بن محمد بن خلدون ولي الدين الحضرمي – دار الفكر – الطبعة الثانية: 1408هـ.

22. سير أعلام النبلاء.

أبو عبد الله شمس الدين محمد بن عثمان بن قايماز التركماني الدمشقي الذهبي – دار الحديث: 1427هـ.

23. شذرات الذهب في أخبار من ذهب.

أبو الفلاح عبد الحي بن أحمد بن محمد بن عماد العكري – تحقيق محمود الأرنؤوط، دار ابن كثير – الطبعة الأولى: 1406هـ.

24. تاريخ أبي الفداء ـ للملك المؤيد إسماعيل بن أبي الفداء.

25. الرحيق المختوم ـ لصفي الرحمن المباركفوري.

26. السيرة النبوية عرض وقائع وتحليل أحداث ـ للدكتور علي محمد الصلابي، وغير ذلك كثير.

## Jerin abubuwan da littafin ya ƙunsa


- Gabatarwa cikin harshen Larabci ............................................2
- Gabatarwa da Hausa .......................................................4
- Larabawa gabanin musulunci ..............................................6
- Addinan larabawa kafin musulunci .......................................6
- Dangantakar Annabi (saw) ..................................................7
- Auren Abdullahi da Amina .................................................8
- Hai'huwar Annabi (saw) ....................................................9
- Alamomin hai'huwar Annabi (saw) ......................................9
- Shayar da Annabi (saw) ....................................................10
- rasuwar mahai'fiyarsa .......................................................11
- Ya dawo ƙarƙashi kulawar kakansa ....................................12
- Ya dawo ƙarƙashin kulawar baffansa ..................................12
- ƙissar Annabi (saw) da Bahira ...........................................12
- Kiwon Timaki ..................................................................13
- Auren Annabi (saw) da Kadija ...........................................14
- Tarayyarsa da ƙurai'shawa wajen gina ................................15
- Annabci .........................................................................15
- Farawar da'awa a sirrance ................................................17
- Darussa .........................................................................18
- Matakin da'awa a bayyane ................................................19
- Hijirar farko zuwa Habasha ..............................................20
- Darussa..........................................................................22
- Musuluntar Hamza ...........................................................23
- Yanke mu'amala da musulmai ............................................24
- Darussa .........................................................................25
- Shekarar baƙin ciki ..........................................................26
- Darussa .........................................................................27
- Auren Annabi (saw) da Saudat ...........................................28

- Fara da’awa a wajen Makka ....................................................28
- Darussa ..............................................................................29
- Isra’i da mi’iraji ....................................................................30
- Darussa ..............................................................................33
- Farawar Musuluncin Ansar ....................................................34
- Darussa ..............................................................................35
- Alamomin hijira ....................................................................36
- taron ƙurai’shawa akan kashe Annabi (saw) ...........................36
- Hijirar Annabi (saw) zuwa Madina ..........................................40
- Shigar Annabi (saw) Madina ..................................................41
- Darussa ..............................................................................41
- Da’awa a Madina ..................................................................43
- ƙulla'Yan’uwantaka tsakanin Muhajirai da ..............................44
- Darussa ..............................................................................44
- Tsarin zamantakewa da yahudawa .........................................45
- Matakin kare kai ...................................................................46
- Yaƙin Badar .........................................................................47
- Darussa ..............................................................................53
- Yaƙin banu ƙai’nuƙa’a ...........................................................54
- Darussa ..............................................................................56
- Yaƙin Uhudu ........................................................................57
- Darussa ..............................................................................64
- Yaƙin banun-Nadir ................................................................66
- Darussa ..............................................................................67
- Yaƙin Ahzab ........................................................................68
- Darussa ..............................................................................74
- Yaƙin banu ƙurai’za ..............................................................75
- Darussa ..............................................................................76
- Yaƙin banu Musɗaliƙ ............................................................77

- ƙiran ƙarya ga A'isha ....................................................................78
- Darussa ........................................................................................80
- Yaƙin Hudai'biyya ........................................................................82
- Darussa ........................................................................................85
- Yaƙin kai'bara ..............................................................................86
- Darussa ........................................................................................88
- Yaƙin fathu Makka .......................................................................88
- Darussa ........................................................................................92
- Yaƙin Hunai'ni ..............................................................................93
- Darussa ........................................................................................96
- Yaƙin Tabuka ................................................................................96
- Darussa ........................................................................................99
- Rashin lafiyar Annabi (saw) ........................................................101
- Siffofin Annabi (saw) da ɗabi'un sa .........................................102
- Matayensa iyayen muminai .........................................................103
- ƳaƳayensa ...................................................................................105
- Kullewa ........................................................................................106
- Jerin littattafan da aka yi muraji'ar su .......................................107